***COURSE GUIDE***

# HAU 311
# SUNAYEN HAUSA


**Course Team** Dr. Ibrahim Garba Gwammaja (Course Writer)-NOUN
Asst Prof. Isa Yusuf Chamo (Editor)-NOUN



**NATIONAL OPEN UNIVERSITY OF NIGERIA**

© 2023 by NOUN Press
National Open University of Nigeria
Headquarters
University Village
Plot 91, Cadastral Zone
Nnamdi Azikiwe Expressway
Jabi, Abuja

Lagos Office
14/16 Ahmadu Bello Way
Victoria Island, Lagos

e-mail: centralinfo@nou.edu.ng
URL: www.nou.edu.ng

All rights reserved. No part of this book may be reproduced, in any form or by any means, without permission in writing from the publisher.

Printed 2023

ISBN: 978-978-058- 656-8

## CONTENT

Gabatarwa (Introduction)………………………………………… iv
Kashe-Kashen Darasi (Study Units)……………………………… iv
Manazarta da abubuwan qara nazari: …………………………….. v
Auna fahimta (Assignment)……………………………………….. v
Jinga (Tutor Marked Assignment)…………………………………. v
Jarrabawa (Final Examination and Grading)……………………. vi
Manufar Wannan Kwas (Course Aim)…………………………….. vi
Koyo Tsantsa (Working Through the Course)…………………… vii
Auna Fahinta……………………………………………………..
Jinga ………………………………………………………………

## GABATARWA (INTRODUCTION)

Wannan darasi na Hau:3313, kwas ne da yake bayani game da al'adun Hausawa na zahiri, waxanda ake iya gani da tavawa da yin amfani da su, musamman dangane da kayayyakin buqatun yau da kullum. Manhanjar darasin tana bayani kan abinda kwas xin ya qunsa, da kuma abubuwan da kwas xin yake bukata, da kuma bayanan da xalibai za su iya yi amfani da su domin fahimtar kwas xin sosai da sosai.

Abubuwan da suke cikin wannan manhaja, abubuwa ne da suka gabatar da wannan darasin, tun daga ma'anar ita kanta kalmar kayayyaki na zahiri waxanda suka danganci al'adun Hausawa na aikace-aikacen cikin gida da wajensa na al'ummar Hausawa. Haka kuma, an yi bayanin yadda ake samar da su, da yadda ake amfani da su, da kuma yadda ake iya gane su, idan an gan su. Ire-irensu sun haxa da kayayyakin abinci da sutura da kwalliya da gine-gine da tafiye-tafiye da sadarwa da makamantansu, waxanda ake amfani da tsirrai (ciyayi da kaba da itatuwa) da qasa (yumvu da tuvaya da vurji) da qarafa da duwatsu.

Manhajar tana bayanin irin abubuwan da suka kamata ga xalibi ya kiyaye a yayin da yake nazartar kowane kashi. Haka nan kuma, manhajar ta kawo tambayoyi waxanda ake bukatar mai nazari ya amsa, don yin haka zai taimaka wajen fahimtar abinda kwas xin yake koyarwa. Yana da kyau idan an sami matsololi ko rashin fahimtar wani kashi ko darasi, a garzaya faxin haka a yayin tattaunawa da malaman da suke kula ko koyar da wannan darasin. Ya zama wajibi a rinqa tuntuvar malami ko malamai kan wasu abubuwan da suka shige wa xalibai duhu, a yayin da ake tattaunawa tsakanin malamai da xalibai (tutorial class). Yin haka zai taimaka ainun wurin samun nasarar isar da sako ga xalibi.

## KASHE-KASHEN DARASI (STUDY UNITS)

Bayanai sun gabata waxanda ke nuna cewa, wannan kwas HAU:313 yana qunshi rukunai huxu ne. Rukuni na xaya yana xauke da kashe-kashe huxu, sannan rukuni na biyu yana xauke da kasha-kashe shida. Haka kuma, rukuni na uku yana xauke da kashe-kashe biyu, sai kuma rukuni na huxu wanda yake xauke da kashe-kashe huxu. Kenan, akwai kashi-kashi har goma sha shida. Ana bukatar a kammala kowane kashi cikin sati guda, wanda ya haxa har da amsa tambayoyi da suke qarshen kowane kashi, da kuma amsa tambayoyin jinga, idan akwai su, a qarshen darasin.

## MANAZARTA DA ABUBUWAN QARA NAZARI:

A qarshen kowane kashi akwai manazarta wanda zai taimakawa xalibai qara nazari da zurfafa bincike. Wasu daga ciki litattafai ne waxanda ba masu wuyar samu ba ne a xakunan sayar da littafai musamman waxanda ke sayar da na Hausa. Akwai littattafan a kan al'adun Hausawa kamar na Alhassan, H. Da Musa, U.I. (1988) da Zarruq, R.M. (1988) da na Sallau, B.A. (2010) da na Soba, S.A. (2015) waxanda ya kamata xalibai su nemo su don su qara karatu. Wasu kuma kundaye ne na kammala karatu digiri na xaya da na biyu harda digirin digirgir, wasu kuma muqalu ne ko dai a Mujallu ko waxanda aka gabatar a tarurukan qara wa juna sani. Wasu daga ciki za a iya samunsa ta kafar sadarwa ta yanar gizo, ko kuma da taimakon xakunan karatu na Jami'o'i, musamman jamai'ar da take kula da "karatu daga gida" idan littattafan sun yi qaranci, ko kuma wuyar samu, to yana da kyau a yi amfani da bayanan da wannan manhajar kwas xin ya samar

## AUNA FAHIMTA (ASSIGNMENT).

Gwaji da ake yi wa xalibai domin gane da fahimtarsu a wannan kwas suna kasancewa ta hanyoyi guda biyu ne. Hanya ta farko ita ce, ta ayyukan da ake ba xalibai su yi domin a gyara. Hanya ta biyu ita ce, wadda ake jarraba xalibai a qarshen zangon karatu (examination). Da yake yanzu komai na koyarwa sun koma ta na'urar mai qwaqwalwa ce, haka ma jingar da ake ba xalibai. Ana ba su ne, kuma suna amsawa da turowa nan take da zarar su gama amsa tambayoyin da aka yi masu. Don haka, ba tare da jimawa ba, za su sami sakamakon jarrabawar da suka yi. Yana da kyau a kiyaye lokaci wajen amsa kowace tambaya, domin yin haka kan taimaka wajen amsa tambayoyi duka cikin lokaci. Ana sa ran xalibai su amsa tambayoyin JINGA aqalla guda uku waxanda daga cikin ukun nan ne za a zavi qwarara guda biyu waxanda xalibi ya fi samun maki don su kasance kashi talatin cikin xari na jararrawa (30%), sauran kashi saba'in (70%) ana samunsu ne a jarrabawar qarshen zangon karatu (semester examination). Ita wannan jarrabawar qarshen zangon karatu, ana yin ta ne ta hayar yanar gizo, saboda haka yana da kyau xalibai su kasance sun gwane da naqaltar na'u'rorin kwamfuta saboda a samu cin jarrabawa yadda ya kamata.

## JINGA (TUTOR MARKED ASSIGNMENT)

Xalibai za su iya gwada fahimtarsu game da wannan kwas ta qoqarin amsa tambayoyin da ke qarshen kowane kashi. Dole kowane xalibi ya san manufar kowane kashi na darussan da suka gabata. Idan ya san haka ne zai iya gwada fahimtarsa ta hanyar amsa tambayoyin da ke biye a kowane kashi. Duk da cewa jarrabawar da ake ba xalibai ta yanar gizo

suke, duk da haka xalibai za su iya gwada fahimtarsu ta qoqarin amsa tambayoyin da ke qarshen kowane kashi.

## JARRABAWA (FINAL EXAMINATION AND GRADING)

Ya kamata xalibi ya sani cewa jarrabawar qarshen zangon karatu na xaukar kashi saba'in (70%) cikin xari na sakamakon da ya kamata xalibi ya samu. Akan ciro tambayoyin da xalibai za su amsa daga cikin ire-iren tambayoyin da ake yi a qarqashin auna fahimta ta qarshen kowane kashi. Don haka yana da kyau xalibai su yi qoqarin amsa waxannan tambayoyin da aka yi masu a qarshen kowane kashi da aka gabatar, ana son a yi amfani da kyakykyawar Hausa da misalai masu kama hankali.

## MANUFAR WANNAN KWAS (COURSE AIM)

Babbar manufar wannan kwas na HAU: 313 ita ce a samar da hanya mai sauqi wadda za ta sanya xalibai su iya gane darasin al'adu na zahiri na al'ummar Hausawa.

Wasu daga cikin manufofin wannan darasi na (HAU: 313) yake qoqarin isar wa ga mai karatu su haxa da:

Da farko, xalibi zai iya sanin al'adun Hausawa na zahiri, waxanda suka danganci kayayyakin da Hausawa suke amfani da su a cikin farfajiyar muhallinsu da suke zaune a ciki.

Haka kuma, xalibai za iya gane kayayyaki na zahiiri na buqatun yau da kullum na Hausawa na gargajiya, tare da iya bambance su da waxanda ban a Hausawa ba.

Kazalika, xalibai za iya sanin yadda ake samar da kayayyakin da suka qunshi al'adu na zahiri na gargajiya na Hausawa, a cikin muhallinsu, daga tsirrai da dabbobi da qasa da duwatsu da qarafa da ruwa da makamantansu,

Haka kuma, nazarin wannan kwas xin zai sanya xalibai su san, tare da gane yadda ake amfani da kayayyakin gargajiya, na zahiri, na al'adun Hausawa da suke samar da su daga muhallinsu da kuma yin amfani da su a kodayaushe.

Daga qarshe, nazarin wannan kwas zai sanya xalibai su san muhimmancin al'adun Hausawa na zahiri, a wajen gudanar da rayuwar Hausawa ta gargajiya a duniyar Bahaushe.

Don cimma wannan manufa, an karkasa wannan kwas zuwa kashi-kashi. Kowane kashi yana xauke da muhimman abubuwa na al'adun zahiri mabambanta na gudanar da rayuwar Hausawa ta yau da kullum.

## KOYO TSANTSA (WORKING THROUGH THE COURSE)

Yana da kyau mai karatu ya nazarci kowane kashi a tsanake tare da bibbiyar manazaratar da aka gabatar domin qarin haske da samun qarin bayanai. Sanannen abu ne cewa Hukumar NOUN ta tanadar wa xalibai muhimman abubuwan da za su tallafa masu a wajen nazarin wannan kwas, irin su xakin karatu, wanda ke xauke da littattafai da wuraren shiga cikin yanar gizo, waxanda za su taimakawa xalibi karatu daga gida. Ba don komai ba take yin haka, sai don inganta karatunsu da kaifafa fahimtar abinda aka sa wa gaba, a wajen cimma manufar wannan kwas.

A qarshen kowane kashi na wannan kwas, akwai tambayoyi. Su waxannan tambayoyin an yi su ne domin su auna fahimtar mai karatu, dangane da abin da ya karanta. Haka nan kuma, akwai ayyukan gida na JINGA (Tutor Marked Assignment) waxanda aka tsara domin xalibai. Ana bukatar idan an amsa waxannan tambayoyi, to, a miqa amsoshin ga malaman da suke kula da darasin, domin a duba, a kuma bayar da sakamakon da ya cancanta. Su waxannan ayyuka na "Jinga," suna taimakawa wajen harhaxa sakamakon jarabawar qarshen zangon karatu, domin fitar da sakamakon kowane kwas da xalibai suka yi. Wannan kwas HAU 313, yana xauke da rukunai guda biyar. A kowane rukuni, akwai kashi guda tara. Saboda haka, ana sa ran xalibai su kammala wannan kwas cikin makwanni goma sha shida, kwatankwacin yawan kasha-kashen da ake da su. Kowane rukuni yana da alaqa da mai bi masa, haka nan kowane kashi yana da dangantaka da mai biye da shi. Saboda haka, kada xalibai su tsallake wani kashi zuwa wani kashi, domin yin haka kan zai gungurta fahimta da rashin gane abin da kwas xin yake koyarwa.

Ana shawartar xalibai su tsaya, su tsara lokacin karatunsu ya dace dai-dai da yawan kashe-kashen da ke cikin kwas xin, domin a sami nasarar kammala kashi-kashin da ke cikin kwas xin, a cikin lokaci. Idan xalibi ya kammala karatu cikin lokaci, yana da damar sake bitar abubuwan da aka yi, a baya, kafin jarabawar qarshen zangon karatu.

Muhimman abubuwan da suka shafi wannan kwas sun haxa da:

a. Rarraba rukunin zuwa kashi – kashi (Study Units)
b. Manazarta da abubuwan kara nazari (Reference and Bibliography)
c. Tambayoyi na auna fahimta (jinga) (Assignment File)

d. Tsarin gabatar da darasi (Presentation Schedule)

Bayan wannan kuma, an tanadi wani sashe domin bayar da ma’anar waɗansu kalmomi da suke da wahalar fahinta.
Domin tafiya da zamani, an sake ƙawata wannan littafin darasi da wasu alamomi kamar haka:

- Alamar da ke nuna gabatarwar darasi a kowane rukuni.
- Alamar da ke nuna manufofin darasi na gaba ɗayan kowane rukuni.
- Alamar da ke nuni da fara shiga cikin darasi a kowane rukuni.
- Alamar da ke nuna taƙaitawa ko ɗaurayar darussan da ke cikin kowane rukuni.
- Alamar da ke nuna jerun littattafan da aka ciro darasi a cikinsu da kuma waɗanda
  ya kamata a tuntuɓa don ƙarin bayani.
- Alamar da take nuna amsoshin da aka kawo na auna fahintar ɗalibai da aka yi a
  - kowane rukuni.

## AUNA FAHINTA

Shi wannan kwas na tsarin da ba ruwanka da malaminka ne, ko na tafi-da-gidanka, shi ya sa ake jarraba fahimtar karatu ta hanyoyi UKU, hanya ta farko ita ce ta auna fahimta a ƙarshen kowane kashin darasi, sannan kowane kashi a ƙarshe ya zo da jinga da za a ba wa ɗalibi. Sai daga ƙarshe a yi jarrabawar ƙarshen zangon karatu, wanda zai nuna an zo ƙarshen darasin.

Auna fahimtar da ake yi a ƙarshen kowane kashi za ta kasance ƙaramar jarrabawa ce, za ta zo da maki 30 daga cikin 100. Ke nan, ana buƙatar ɗalibi ya amsa tambayoyi uku inda za a zaɓi 2 su kasance su ke ɗauke da maki 30, maki 15 ga kowace tambaya. Sauran maki 70 za su zo ne a jarrabawar ƙarshen kwas.

Jarrabawa dai kamar kullum za a gabatar da ita ne daga gida, ita ma ba a cikin cikin aji ba, kuma za ta kasance ta Intanet ne, ke nan ilimin na’ura mai ƙwaƙwalwa abu ne mai muhimmanci ga ɗalibi.

## JINGA

Jingar aji tamkar gwajin jarrabawa ne ga ɗalibi, saboda haka amsa jingar da ke ƙarshen kowane kashin darasi zai ba wa ɗalibi damar fahimtar yadda jarrabawar ƙarshe za ta kasance. Yana da kyau ɗalibi ya mayar da hankali domin amsa irin samfurin waɗannan tambayoyi, domin za su sauƙaƙa amsa tambayoyin jarrabawa a ƙarshen darasin baki ɗaya

## Jarrabawar Ƙarshen Kwas

Ita dai jarrabawa ita ce hanyar da ake gane ko ɗalibi ya gane darasi ko kuma ya samu naƙasu a wani ɓangare, saboda haka tana ɗauke da kaso mafi tsoka na 70 cikin 100. Ba wani dabo a cikin wannan fasali domin ana ɗauko samfurin jarrabawar ne daga tambayoyin da aka dinga turawa na auna fahimta da kuma jinga. Ke nan mayar da hankali wajen amsa waɗannan tambayoyi a lokacin darasi zai rage zafin tambayoyin ƙarshen darasi.

**MAIN COURSE**

## CONTENTS


| | | |
|---|---|---|
| **Rukuni Na Ɗaya (1)** | **……………………………………….** | **1** |
| Kashi Na Ɗaya (1) | Haihuwa A Wajen Bahaushe……….. | 1 |
| Kashi na Biyu (2) | Wasu Hidimomin da ake yi Bayan Haihuwa…………………………….. | 8 |
| Kashi na Uku (3) | Sunayen Hausawa …………………. | 14 |
| Kashi na Huɗu (4) | Sunayen Hausawa na Gargajiya…….. | 24 |
| **Rukuni Na Biyu (2)** | **……………………………………….** | **32** |
| Kashi na Ɗaya (1) | Sunayen Hausawa Bayan Zuwan Musulunci…………………………… | 32 |
| Kashi na Biyu (2) | Sunayen Ahalin Annabi Muhammad (SAW)……………………………….. | 41 |
| Kashi na Uku (3) | Sunayen Manyan Mata da Waliyyai. | 48 |
| Kashi na Huɗu (4) | Wasu Sunayen Hausawa Bayan Zuwan Musulunci…………………… | 53 |
| **Rukuni Na Uku(3)** | **…………………………………..…** | **58** |
| Kashi na Ɗaya (1) | Wasu Sunayen Hausawa…………… | 58 |
| Kashi na Biyu (2) | Wasu Sunayen Hausawa…………… | 63 |
| Kashi na uku (3) | Wasu Sunayen Hausawa…….……… | 67 |
| Kashi na Huɗu (4) | Ƙirar Sunayen Hausawa……………. | 72 |
| **Rukuni Na Huɗu (4)** | **……………………………………….** | **78** |
| Kashi na Ɗaya (1) | Ƙirar Sunayen Hausawa……………. | 78 |
| Kashi na Biyu (2) | Ƙirar Sunayen Hausawa…………….. | 85 |
| Kashi na uku (3) | Sunayen Hausawa na Dangantaka….. | 91 |

# RUKUNI NA ƊAYA (1)

Kashi Na Ɗaya (1) Haihuwa A Wajen Bahaushe
Kashi na Biyu (2) Wasu Hidimomin da ake yi Bayan Haihuwa
Kashi na Uku (3) Sunayen Hausawa
Kashi na Huɗu (4) Sunayen Hausawa na Gargajiya

## Kashi Na Ɗaya (1) Haihuwa A Wajen Bahaushe

**Abubuwan da Suke Ciki**

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufofi Darasi
1.3 Ma'anar Haihuwa
  1.3.1 Hidimomin da ake yi Kafin Haihuwa
  1.3.2 Hidimomin da ake yi Bayan Haihuwa
1.4 Taƙaitawa
1.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
1.6 Manazarta
1.7 Amsoshin Auna Fahimta

## 1.1 Gabatarwa

A kashin farko na wannan darasi za mu yi ƙoƙari wajen bayyana wa ɗalibai abin da ake nufi da al'ada da asalin kalmar Haihuwa da kuma yadda haihuwa take wajen Hausawa. Wannan zai taimaka wa ɗalibai su fahimci inda darasin ya dosa. Wannan darasi zai yi ƙoƙarin fayyace abun da ake nufin da haihuwa a fagen nazari, da abubuwan da bisa al'ada ake yi kafin da kuma bayan an haihu a wajen Hausawa. Hakan zai bayar da haske ga ɗalibai su san ainihin yadda haihuwa take a wajen Hausawa.

## 1.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi ɗalibai za su iya:

- Bayyana ma'anar kalmar Haihuwa.
- Zayyana hidimomin da ake yi kafin haihuwa.
- Bayani kan hidimomin da ake bayan haihuwa.
- Kawo Alamomin haihuwa

## 1.3 Ma'anar Haihuwa

Dangane da abin ya shafi ma'anar haihuwa kuwa, a nan ana iya cewa akwai ra'ayoyi mabambanta dangane da ma'anar haihuwa. Ga kaɗan daga cikin abin da masana suka ce dangane da ma'anar haihuwa. Abdullahi (2008:225), ya rawaito cewa Alhassan da wasu sun bayyana haihuwa a matsayin "ya yin da miji da mata suka ƙaru da samun ɗa ko'ya.

A ma'anar Ƙamusun Hausa (2006: 189), ya bayyana ma'anar haihuwa da cewa: 'samun ɗa ko 'ya bayan mace ta yi ciki wata tara'. Haka kuma a wani ra'ayin, haihuwa:

> Ƙaruwa ce ta hanyar fitowar wani abu mai rai daga jikin wata halitta jinsin mace wanda ya ɓoyu a wani wuri na musammam na wani ƙayyadadden lokaci don samun kamanni ko siffa kwatankwacin na zuriyarsu, wanda ke aukuwa a sakamakon saduwa da jinsin namiji na wani halittar (Abdullahi, 2008:228).

Bisa ga waɗannan ma'anoni, za mu iya cewa haihuwa tana nufin samun ɗa ko 'ya a tsakanin ma'aurata (namiji da mace).

### 1.3.1 Hidimomin da ake yi Kafin Haihuwa

A bisa tsarin al'adun Hausawa, akwai tanade-tanaden da mazaje magidanta kan yi domin tarbon abin da za a iya haifa masu da zarar mutum ya fahimci cewa matarsa ta sami juna biyu. Daga cikin ire-iren kayayyakin da ake tanada kuwa, masana sun kawo su kamar haka:

#### 1.3.1.1 Al'adar Goyon Ciki

A ƙasar Hausa, ana da al'adar mayar da yarinya ta haihu a gidansu idan cikin ya kai wata bakwai, kuma galibi wannan na faruwa ne ga mace mai haihuwar fari. Wannan al'ada ana yin ta ne domin mai ciki ta sami kulawa ta musammam a gidansu. A wannan lokacin ana kula da lafiyarta, kuma ana sanya mata wasu sharuɗɗa na hani ko horo ga aikata wasu ayyuka ko cin wani abu musammam waɗanda za su taimaka mata sauka lafiya.

#### 1.3.1.2 Samar da Magungunan Dauri

Waxannan magunguna ne da miji ke tanadar wa matarsa ko kuma iyayen miji ko na matar su tanada domin bai wa mai juna biyu ta sha musamman idan cikin ya kai kimanin wata bakwai zuwa haihuwa. Amfanin magungunan shi ne domin ta sami sauƙin haihuwa.

Magungunan za su wanke zaƙi da maicon da ke cikin ciki na mai juna biyu, wanda hakan zai sanya ta sami sauƙin naƙuda a lokacin haihuwa.

### 1.3.1.3 Tanadar Itacen Wanka

A bisa al'ada maigida yakan tanadi itacen wanka ga matarsa, zarar ya ga lokacin haihurta ya kusa ma'ana, idan ciki ya shiga wata na tara ko ya tsufa. Akan tanadi itacen da yawa domin ba wanka kawai za a rinƙa yi da itacen ba, har ma da sauran wasu abubuwa kamar, dafa abinci da sauran harkoki na gida.

### 1.3.1.4 Kayan Barka

Waɗannan kayayyaki ne da suka danganci suturar maijego da abin da ta haifa. Maigida zai tanade su ne tun kafin a haihu ko kuma bayan an haihu. Daga cikin kayan akwai turamen atamfa da kayan jinjirai da turare da man shafawa da kitso da sauransu. Magidanci kan hakan gwargwadon halinsa.

**AUNA FAHIMTA NA 1**

| | |
|---|---|
| 1. | Me ka Fahimta da kalmar haihuwa? |
| 2. | Kawo hidimomin guda biyu kafin haihuwa |
| 3. | Ya ya al'adar goyon ciki take a wajen Hausawa? |
| 4. | Waɗanne irin kayayyaki ake amfani da su a kayan barka? |

## 1.4 Hidimomin da ake yi Bayan Haihuwa

A tsari na al'adun Hausawa, akwai kuma tanade-tanaden da mazaje wato, magidanta sukan yi domin nuna farin ciki da abun da Allah ya ba shi. Abubuwan na da dama amma ga wasu kaɗan daga ciki:

### 1.4.1 Gara

Kamar yadda Ƙamusun Hausa ya bayyana cewa, kalmar gara na nufin *kaya, musamman na abinci da iyayen mai haihuwa kan kai wa 'yarsu bayan an gama bukin aure ko haihuwa. (*CNHN 2006:157). Haka kuma za mu iya cewa gara ta ƙunshi wasu kayayyaki da iyayen maijego suke samarwa su kawo mata. Kayayyakin sun haɗa da: shinkafa da gero da dawa da man girki da gishiri da maggi da daddawa da man shanu da alkaki da sauransu.

### 1.4.2 Itacen Biƙi

Maigida zai fara tanadin itatuwan da za a yi amfani da su a wajen shagulgulan wankan jego har zuwa bukin suna da kuma kwanakin da mai jego za ta yi tana wankan ruwan zafi.

### 1.4.3 Kayan Barka

Waɗannan kayayyaki ne da suka danganci suturar maijego da abin da ta haifa. Maigida zai tanade su ne tun kafin a haihu ko kuma bayan an haihu. Daga cikin kayan akwai turamen atamfa da kayan jinjirai da turare da man shafi da kitso da sauransu da dama gwargwadon halin magidanci.

### 1.4.4 Taron Suna

Taro ne da 'yanuwa da abokanin arziki inda za su taru domin taya murna ga mahaifin jinjiri da maijego a ranar da aka cika kwana bakwai da haihuwar jinjiri. maza sukan taru ne a kofar gida, su kuwa mata suna zama a cikin gida ne domin hidimar shirya abinci ga baƙin da suka halarci bukin.

### 1.4.5 Yanka Dabbar Suna

Dabbar suna, dabba ce da akan tanada domin a yanka ta hanya tabbatar wa da jinjiri suna yanka. Galibi a ƙasar Hausa akan yanka Rago ko Tumaki ko Awaki ko ma a wasu lokuta Shanu a wajen zanen suna. Da zarar an yanka dabbar suna da nufin a sanya suna iri kaza ga jinjirin.

### 1.4.6 Tsagar Gado

Wannan tsaga ce da ake yi a tsakanin Hausawa domin a nuna irin ƙabilar da mutum ya fito daga cikin rukunin Hausawa. Misali, akwai Zamfarawa da Kabawa da Katsinawa da Kanawa da Zazzagawa da sauransu. A bisa al'ada akan yi wa abin da aka haifa tsagar gado ne tun ranar bukin sunansa.

### 1.4.7 Wasannin Gado a Ranar Suna

Wasanni ne da suka shafi martaba irin gadon gida ko sana'o'in da mutum ya tashi a cikinsu. Misali idan a gidan Mahauta ne akan yi wasan hawan ƙaho, ko kuma a yi wasa da wuta idan a gidan maƙera ne da sauransu.

### 1.4.8 Abincin Gara

Wannan abinci ne da ake yi na musamman domin bukukuwan aure ko suna a ƙasar Hausa. Galibi irin wannan abinci ya shafi masa (waina) da alkaki da duɓulan da Fanke da naman kaji. Akan raba wa mutanen da suka zo shaidar raɗin sunan domin su ci, kuma su tafi da shi a gidajensu.

**AUNA FAHIMTA NA 2**

1. Kawo misalai uku hidimomin da ake yi bayan haihuwa.
2. Me ake nufi da abincin gara?
3. Wanne dalili ne ya sa ake wasannin gado?
4. Yi ɗan tsokaci kan taron suna.

## 1.5 Taƙaitawa

A taƙaice wannan kashin ya tattaro bayanai waɗanda suka danganci al'adu waɗanda suka bayani kan haihuwa da kuma ire-iren tanade-tanaden da ake yi mata kafin da bayan an yi haihuwar.

## 1.6 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi

1. Tsagar gado – tsaga ce da ake yi domin nuna asali ko tushen mutum
2. Kayan gara – Kayayyakin abinci kamar gero da shinkafa da masara da mai da sauransu, su ne ake kaiwa maijego
3. Ragon suna – Rago ne da ake sayowa domin yankawa ga jaririn da aka haifa.

## 1.7 Manazarta


Abdullahi I.S.S (2008). *Jiya ba Yau Ba: Waiwaye a Kan Al'adun Matakan Rayuwar*

*Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa*. Kundin digiri na uku: Jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto.

Adamu, M. T. (2015). Tasirin Musulunci Kan Sunayen Hausawa. A Cikin *Harsunan Nijeriya*, Vol. XXV: 163-186.

Alhassan da Wasu (1987). *Zaman Hausawa.* Zaria: ABU Press.

Bichi A.Y (2013). Tsokaci a Kan Bukukuwan Hausawa na Gargajiya wajen cigaban

Al'umma. Zaria: Ahmadu Bello University, Press.

CNHN (2006). Ƙamusun Hausa.Kano: Jami'ar Bayero, Kano

CNHN (1981). Rayuwar Hausawa. Lagos: Thomos Nilson Nigeria Limited.

Gusau, G.U (2012). Bukukuwan Hausawa. Gusau: Ol-Faith Prints.

## 1.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahinta

**Amsoshin auna fahimta na 1:**

1. Haihuwa shi ne samun ɗa ko 'ya bayan mace ta yi ciki wata tara', ko ya yin da miji da mata suka ƙaru da samun ɗa ko'ya.
2. Hidimomin da ake yi kafin haihuwa sun haɗa da:
    - i. Goyon ciki
    - ii. samar da magungunan dauri
    - iii. tanadar itacen wanka
    - iv. kayan barka
3. Al'ada ce ta mayar da yarinya ta haihuwa a gidansu idan cikin ya kai wata bakwai, kuma galibi wannan na faruwa ne ga mace mai haihuwar fari. Wannan al'ada ana yin ta ne domin mai ciki ta sami kulawa ta musammam a gidansu
4. Kayan barka sun haɗa da:
    - i. turamen
    - ii. atamfa
    - iii. kayan jinjirai
    - iv. turare
    - v. man shafawa da kitso

**Amsoshin auna fahimta na 2:**

1. Hidimomin da ake yi bayan haihuwa sun haɗa da:
    - i. gara
    - ii. itace buki
    - iii. kayan barka
    - iv. taron suna
    - v. yanka dabba
    - vi. tsagar gado
2. Wannan abinci ne da ake yi na musamman domin bukukuwan aure ko suna a ƙasar Hausa. Galibi irin wannan abinci ya shafi masa (waina) da alkaki da duɓila da Fanke da naman kaji. Akan raba wa mutanen da suka zo shaidar raɗin sunan domin su ci, kuma su tafi da shi a gidajensu.
3. Abubuwan da suke haifar da wasannin gado a ranar suna sun haɗa da:
    - i. gadon gida
    - ii. sana'o'in da mutum ya tashi a cikinsu.
4. Taro ne da 'yanuwa da abokanin arziki inda za su taru domin taya murna ga mahaifin jinjiri da maijego a ranar da aka cika kwana bakwai da haihuwar jinjiri. maza sukan taru ne a kofar gida, su kuwa mata suna zama a cikin gida ne domin hidimar shirya abinci ga baƙin da suka halarci bukin.

# Kashi na Biyu (2) Wasu Hidimomin da ake yi Bayan Haihuwa

**Abubuwan da Suke Ciki**

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufofi Darasi
2.3 Ma'anar Ranar Zanen Suna
 2.3.1 Yadda ake Raɗa Suna a Ƙasar Hausa
 2.3.2 Abubuwan da Ake Amfani da su Wajen Raɗa Suna
 2.3.3 Bukin Suna
2.4 Ra'ayoyin Masana Kan Raɗin Suna
2.5 Taƙaitawa
2.6 Manazarta
2.7 Amsoshin Auna Fahimta

## 2.1 Gabatarwa

A kashi na ɗaya na wannan rukuni mun kawo bayanai kan haihuwa da kuma hidimomin da ake yi kafin da kuma bayan haihuwa a wajen Hausawa amma, a wannan kashin za mu tattauna a kan irin hidimomin da ake gudanarwa a ranar suna ko ranar da ake raɗa wa jariri suna a bisa al'ada ta Hausawa. Wannnan kashi za ya kawo bayanai kan yadda Hausawa suke gudanar da raɗa wa jariri suna.

## 2.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashin ɗalibai za su iya:

- Bayani kan Ranar Zanen Suna.
- Kawo yadda ake raɗa suna a ƙasar Hausa.
- Zayyana abubuwan da ake dubawa wajen Raɗa Suna.
- Bayyana ra'ayin masana kan ranar suna

## 2.3 Ranar Zanen Suna

A da can game da al'adun Hausawa dangane da ranar suna kuwa akwai bambance-bambance a tsakanin wani ɓangare da wani ɓangare a cikin ƙasar Hausawa. Amma sai dai dukkansu sun haɗu a ɓangare yin ƙauri. Wasu daga cikin Hausawa idan namiji aka Haifa a kan dafa ƙaurinsa ranar da ya kwana uku a duniya, idan mace ce sai ranar da ta kwana huɗu, kuma ranar za a raɗa masa ko mata suna.

### 2.3.1 Yadda ake Raɗa Suna a Ƙasar Hausa

i- A wasu wuraren kuwa musamman a yankin Sumaila da Rano da Ƙiru na ƙasar Kano a kan yi wa jariri aski da tsaga ranar shan ƙauri. Kuma wani babba a dangi shi zai bayar da sunan yaron ko yarinyar amma ba za a faɗa wa kowa ba sai ranar da aka kwana bakwai.

ii- A ƙasar Katsina kuwa a da, musamman waɗanda suke zaune a kudancin Katsina ba ruwansu da taron suna bayan kwana uku ko bakwai. Su kuwai idan mace ta haihu sai dangin mijin su kawo kaji guda biyu ko uku na ƙauri a dafa wa mai jego, bayan wannan babu wani abu da ake yi sai bayan kwana arba'in sai a yi wani biki da suke kira "***kantsaki".*** Kuma, mata ne kawai suke taruwa kowacce ta zo wa mai jego da gudummawarta. Za a yanka ɗan-taure a yi abinci a cicci, kuma kafin a waste matan za su yi tunanin lokacin da aka haifi jaririn ko yanayin haihuwar su bayar da suanan ta haka.

iii- Su kuwa a da, Hausawa gundumar Dutsen-ma ta ƙasar Katsina idan mace ta haihu ba ta da damar fita daga ɗakinta sai bayan kwana goma sha bakwai, kuma wannan ita ce ranar raɗa suna. Dattijai kamar guda goma za su taru a gidan da aka yi haihuwar, sai a samo gaɓar kara a tsaga biyu, a jikin kowane tsagi sai a yi wasu zane-zane irin na bayan ƙwayar ko kuma jarfa. Idan an gama sai a ba wata tsohuwa ta kai wa mai jegon ta zaɓi ɗaya daga ciki. Sai tsohuwar ta dawo wa da dattijan wanda aka zaɓa, to su da sun duba ɗan sun san sunan da ta zaɓa, sai su ce tsohuwa ta koma ta gaya wa mai jego sunan jariri kaza, amma kada ta kuskura ta gaya wa kowa sai ranar kwana arba'in. wato kenan ban da dattijai da tsohuwa da mai jego ba wanda ya san sunan jariri sai an yi arba'in wato ranar mayar da mahaifa.

iv- Amma Hausawa da suke zaune a gundumar Kwatarkwashi a Zamfara, a da can babu ruwansu da tsayar da wata rana taƙaimaimai ta raɗa suna. Su a wurinsu ba a raɗa suna sai lokacin da kaka ko uban jariri ya sami hali ko za a shekara nawa. A wani lokacin har akan sami mutum ya isa mizalin aure amma ba a yi masa sun aba, sai ya rinƙa amsa sunan kakanni. Wato kamar su a koke, hana aiki, kumatu da 'yar mutsila da dai sauransu. Amma dai abun kunya ne don kuwa har gori akan yi wa mutum cewa ya gaza.

### 2.3.2 Abubuwan da ake dubawa Wajen Raɗa Suna

Amma kuma duk da ’yan bambance-bambancen da ake samu na ranar suna, sai dai yawancin irin sunayen da ake amfani da su ga jariri namiji ko mace kusan iri ɗaya ne.

Yawancin sunayen Hausawa na maza dana mata ana duban lokaci ko yanayi, saffa ko sanadin da ya kama a lokacin aure ko kuma haihuwar sai a ambaci jariri da haka:

Zanen suna al’ada ce da Bahaushe ke bi yana yankawa abin haihuwa wanda ka iya zama yaro ko yarinya suna.

**Auna fahimta na 1**

1. Shin akwai bambance-bambance na raɗin suna a tsakanin Hausawa?
2. Raɗin suna a tsakanin Hausawa ya kasu gida______
3. Kawo misalan raɗin suna a tsakanin Hausawa guda biyu kawai.
4. Waɗanne abubuwa ake amfani da su a wajen raɗa suna?

### 2.4 Bukin Suna

Ta fuskar bikin suna a wajen Hausawa kuwa, akan yi shi hawa-hawa. Akwai wanda ake yi nan-take da zarar an raɗa sunan. Akan fito da abinci don jama’ar da suka taru su ci, su kuma maroƙa da makaɗa suna kaɗe-kaɗensu, ana ba su abin masarufi.

Bayan kuma an gama wannan, sai su ma mata sukan haɗu tun daga lokacin da rana ta fito har zuwa maraice, suna kuma yin ’yan kaɗe-kaɗe, da waƙe-waƙensu na mata, suna guɗa da sauransu. Sannan kuma sukan zo da kyaututtuka a matsayin gudummawa ga ita mai haihuwar. Wannan taro na mata bai cika kaiwa faɗuwar rana ba.

Idan kuma haihuwar fari ce, to, akan samu mata su taru a gidan iyayen mai jego; wato gidan mata kenan, su haɗo nasu abubuwan. Bayan sun tattara abubuwan da suka tara, sai kuma su ɗauko shi da maraice zuwa gidan da aka yi haihuwa, gidan maza kenan, su zo su rarraba ga iyaye, da sauran dangin miji. Wannan rabo shi ake kira tsaraba.

Akan samu saɓawar wasu abubuwa daga wani gidan zuwa wani ko kuma daga wani yankin zuwa wani yankin wanda ka iya zama ƙari ko ragi a kan abubuwan da aka zayyana a cikin wannan rubutun.

## 2.5 Ra'ayoyin Masana Game da Ranar Suna

Farfesa Bunza (2002), ya ruwaito cewa wannan al'ada daɗaɗɗiyar al'ada ce da ta wanzu a Ƙasar Hausa tun kafin kowane sauƙaƙƙen addini. Ana yin wannan al'ada ne ta hanyar samun wasu dattawa/dattaɓai su yi zane-zane a jikin kararen rama ɓararru guda bakwai, sannan sai a ɗauka a kaiwa maijego, wanda duk ta zaɓa sai a yi amfani da zanen da ke jikinsa a raɗa wa jaririn ko jaririyar suna.

Wannan al'ada ta zanen-suna ta samu sauye-sauye da dama. Daga ciki akwai sauyin farko da ta samu yadda ya koma kawai jama'a na taruwa a ƙofar gidan da aka yi haihuwa, sai a rarraba musu goro da sauraran abubuwan da suka samu, kamar alawa da dabino, sannan liman ya ce an sawa yaro ko yarinya suna wane ko wance. Sai kuma maroƙi ya faɗa da ƙarfi kowa ya ji. Sannan a yi addu'a, sai kuma kowa ya watse.

Su kuma yara a lokacin da ake yin wannan addu'a, sai su ruga da gudu su shiga cikin gida wajen mata su gaya musu cewa an saka wa jariri ko jaririya suna wane ko wance. A lokacin da suke gudun suna ambatar Allah ya raya wane ko wance. Duk yaron da ya yi sauri ya fara isa ya je ya sanar cewa wane ko wance aka saka, akan bashi tukuici wanda kuɗaɗe ne da alewa da goro amma ba masu yawa ba.

Sai kuma a halin yanzu da Musulunci ya yi ƙarfi, a mafiya yawan gurare musamman birane, ba a ma taruwar sai dai a raɗa sunan a masallaci.
A ranar suna, ana yanka rago a raba goro, liman ya yi wa jariri huɗuba galibi bayan kwana bakwai da haihuwa, duk da yake ana iya huɗuba tun ranar da aka haifi jinjiri a raɗa wa yaro suna sai dai ba za a bayyana sunan ba sai ranar suna. Galibi da yake Hausawa mabiya addinin Musulunci ne, don haka, ana zaɗen sunan ne daga cikin sunayen addinin

Musulunci.

> Ranar raɗin suna, za a taru tsakanin dangin mai haihuwa da mijinta. Idan waɗanda duk ake jira sun taho, za a raba goro ga jama'a inda za a fara fitar da na malamai da wanzamai da mata. Daga nan sai liman ya yi wa abin haihuwar addu'a da ita kanta mahaifiyar da uban da sauran jama'a baki ɗaya. (Yahaya da wasu, 2001:99)

Shi kuwa Gusau (2012:42) Yana da ra'ayin cewa:

> Zanen suna ko raɗin suna ana gudanar
> da shi ga abin da aka haifa, bayan mako
> ɗaya da haihuwa. Zanen suna ko raɗin
> suna ya kasu kashi biyu, akwai zanen
> suna a gargajiyance, akwai kuma zanen
> suna a addinance.

## Auna fahimta na 2

| | |
|---|---|
| iii- | Wannan al’ada daɗaɗɗiyar al’ada ce da ta wanzu a Ƙasar Hausa tun kafin kowane sauƙaƙƙen addini. Wane ne ya faɗi hakan? |
| ii- | A kudancin Katsina ba ruwansu da taron suna bayan kwana______ |
| iii- | Kawo abubuwa guda uku da ake rabawa ranar raɗin suna? |
| iv- | Su waye suke zane-zane a jikin kararen rama ɓararru guda bakwai? |

## 2.6 Taƙaitawa

A taƙaice wannan kashin ya tattaro bayanai waɗanda suka danganci yadda ake raɗin suna dangane da wasu al’adu na Hausawa. Akwai wasu ala’adu waɗanda suka shafi al’ada da kuma addini, sannan an kawo wasu hidimomi waɗanda ake gudanarwa a ranar zanen suna tare da kawo wasu ra’ayoyi na masana dangane da raɗin suna.

## 2.7 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi

- kantsaki – gudummawar da mata suke kaiwa mai jego.
- Kwatarkwashi- sunan gari ne a ƙasar Zamfara
- Huɗuba - addu’o’in da liman
- Tukuici – ladan da akan ba wanda ya kai wata kyauta don nuna yabawa

## 2.8 Manazarta


Abdullahi I.S.S (2008). “Jiya ba Yau Ba: Waiwaye a Kan Al’adun Matakan Rayuwar

Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa.” Kundin digiri na uku: Jami’ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto.

Adamu, M. T. (2015). Tasirin Musulunci Kan Sunayen Hausawa. A Cikin *Harsunan Nijeriya*, Vol. XXV: 163-186.

Alhassan da Wasu (1987) *Zaman Hausawa.* Zaria: ABU Press.

Bichi A.Y (2013). *Tsokaci a Kan Bukukuwan Hausawa na Gargajiya wajen cigaban Al’umma*. Zaria: Ahmadu Bello University, Press.

CNHN (1981). *Rayuwar Hausawa*. Lagos: Thomos Nilson Nigeria Limited.

Gusau, G.U (2012). *Bukukuwan Hausawa*. Gusau: Ol-Faith Prints.

## 2.9 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahinta

Amsoshin auna fahimta na 1:

1. Shin akwai bambance-bambance na raɗin suna a tsakanin Hausawa?
   Amsa :- Haka ne

2. Raɗin suna a tsakanin Hausawa ya kasu?
   Amsa: - Gida huɗu (4)

3. Kawo misali daga ɓangare biyu kawai.
   Amsa: -
   i. A wasu wuraren kuwa musamman a yankin Sumaila da Rano da Ƙiru na ƙasar Kano a kan yi wa jariri aski da tsaga ranar shan ƙauri. Kuma wani babba a dangi shi zai bayar da sunan yaron ko yarinyar amma ba za a faɗa wa kowa ba sai ranar da aka kwana bakwai.
   ii. Amma Hausawa da suke zaune a gundumar Kwatarkwashi a Zamfara, a da can babu ruwansu da tsayar da wata rana taƙaimaimai ta raɗa suna. Su a wurinsu ba a raɗa suna sai lokacin da kaka ko uban jariri ya sami hali ko za a shekara nawa. A wani lokacin har akan sami mutum ya isa mizalin aure amma ba a yi masa suna ba, sai ya rinƙa amsa sunan kakanni. Wato kamar su a koke, hana aiki, kumatu da 'yar mutsila da dai sauransu. Amma dai abun kunya ne don kuwa har gori akan yi wa mutum cewa ya gaza.
4. Waɗanne abubuwa ake duba a wajen raɗa suna?
   Amsa: - Ana duba *lokaci* ko *yanayi*, *siffa* ko *sanadin* da ya kama a lokacin aure ko
   kuma haihuwar sai a ambaci jariri da haka:

**Amsoshin auna fahimta na 2:**

1. Wannan al'ada daɗaɗɗiyar al'ada ce da ta wanzu a Ƙasar Hausa tun kafin kowane
   sauƙaƙƙen addini. Wane ne ya faɗi hakan?
   Amsa:- Farfesa Bunza (2002)
2. A kudancin Katsina ba ruwansu da taron suna bayan kwana_____
   Amsa: - uku ko bakwai
3. Kawo abubuwa guda uku da ake rabawa ranar raɗin suna.
   Amsa: - goro da alawa da dabino
4. Su waye suke zane-zane a jikin kararen rama ɓararru guda bakwai?
   Amsa: - Dattawa

## Kashi na Uku (3) Sunayen Hausawa

**Abubuwan da Suke Ciki**

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufofi Darasi
3.3 Sunayen Hausawa
3.4 Ire-Iren Sunayen Hausawa
3.4.1 Sunayen Hausawa na Gargajiya
3.4.2 Sunayen Hausawa na Zamani
3.5 Sunayen Hausawa na Lokaci
3.5.1 Sunayen Maza na Lokaci
3.5.2 Sunayen Mata na Lokaci
3.6 Taƙaitawa
3.7 Ma’anar Kalmomi
3.8 Manazarta
3.9 Amsoshin Auna Fahimta

### 3.1 Gabatarwa

A cikin kashin da ya gabata, mun kawo bayanai kan ranar zanen suna da kuma yadda ake raɗa suna a ƙasar Hausa. An kuma kawo abubuwan da ake amfani da su wajen raɗa suna da yadda ake yin bukin suna da kuma ra’ayoyin masana game da ranar suna amma, a wannan kashin za mu tattauna a kan ire-iren sunayen Hausawa.

### 3.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashin ɗalibai za su iya:

- Bayani kan sunayen Hausawa.
- Kawo ire-iren sunayen Hausa.
- Zayyana sunayen Hausa na lokaci da na yanayi.
- Bambance sunayen Hausa na lokaci da na yanayi.

### 3.3 Sunayen Hausawa

Hausawa a wurare irinsu Arewancin Nijeriya da Jamhuriyar Nijar da Sudan da Ghana da wasu ƙasashe na da wata tabi’a da aka sansu da ita ta sanyawa ’ya’yansu sunayen waɗanda suka shafi sunayen gargajiya da na zamani waɗanda suka haɗa da: sunayen Musulunci, kamar sunayen siffofin Allah da na Annabawa Mala’iku da Sahabbai da sauransu.

Kamar yadda muka gani wajen ƙirƙirar ko zanen suna, Al’ummar Hausawa suna la’akari ne da halin da haihuwa ta zo ko ta samu, don

haka za a iya karkasa sunayen Hausawa na gargajiya kashi-kashi kamar haka:

## 3.4 Ire-Iren Sunayen Hausawa

Dangane da ire-iren sunayen Hausawa an kasa su zuwa gida biyu, na gargajiya da na zamani ko bayan zuwan Larabawa da Turawa. Ga su kamar haka:

### 3.4.1 Sunayen Hausawa na Gargajiya

A ƙarƙashin sunayen Hausawa na gargajiya akwai wasu muhimman abubuwa da ake amfani su, kamar lokaci ko yanayi ko sanadi da kuma siffar da aka haifi jariri. Ga misalai:

SUNAYEN LOKACI

SUNAYEN SANADI


SUNAYEN YANAYI

SUNAYEN SIFFA

ZANEN FARKO

### 3.4.2 Sunayen Hausawa Bayan Zuwan Musulunci

A wannan kashin akwai rukuni guda biyu, sunayen Hausawa waɗanda ake amfani da su bisa la'akari da sunayen Allah da siffofinsa da Annabi Muhammad da na Annabawa da Mala'iku da na sahabban Annabi da sauransu.




**ZANEN BIYU**

Sai kuma sunayen na al'ada da Hausawa suke amfani da su wadanda suka shafi sunaye na ranaiku da na sha'awa ko ra'ayi, su kuma ga su kamar haka:




**ZANE NA UKU**

## 3.5 Sunayen Hausawa na Lokacin Haihuwa

A irin waɗannan sunayen Hausawa ana la'akari da lokacin da aka haifi jariri, ma'ana za a yi la'akari da da rana (safiya ce ko rana ko dare) ko kuma watan da aka haifi jariri ko kuma shekarar da aka haifi jaririn. Ire-iren sunayen da ake samu a ƙarƙashin wannan sun haɗa da sunayen maza da mata.

### 3.5.1 Sunayen Maza

Sunayen maza waɗanda ake yi amfani da lokacin da aka haifi jaririn, a wajen sanya masa suna. Ga sunayen maza na lokaci da ma'anarsu:

| SUNA | MA'ANA |
|---|---|
| Hantsi | Yaron da aka Haifa da hantsi |
| Ranau | Yaro ko yarinyan da aka Haifa da rana |
| Dare/Baƙo | Yaro ko yarinyan da aka Haifa da daddare |
| Sammako | Yaro ko yarinyan da aka Haifa da sassafe |
| Hazo | Yaron da aka Haifa a lokacin ɗari |
| Damina | Yaron da aka Haifa a lokacin damina |
| Anaruwa | Yaron da aka Haifa a lokacin ruwa |
| Nomau | Yaron da aka Haifa a lokacin noma |
| Magawata | Yaron da aka Haifa a farkon wata |
| Ɗankaka/ Ɗan Yalwa | Yaron da aka Haifa a lokacin kaka |
| Dare | Yaron da aka Haifa da daddare |
| Kosau/Wada/Wadaci | Yaron da aka Haifa a lokacin wadata |

### 3.5.2 Sunayen Mata

Sunayen mata waɗanda ake yi amfani da lokacin da aka haifi jaririyar, a wajen sanya mata suna. Ga sunayen mata na lokaci da ma'anarsu:

| SUNA | MA'ANA |
|---|---|
| Tashuka | Yarinyar da aka Haifa a lokacin shuka |
| Marka | Yarinyar da aka Haifa a lokacin marka-marka |
| Baƙuwa | Yarinyar da aka Haifa da daddare |
| Kakale/'Yarkaka | Yaro ko yarinyan da aka Haifa da sassafe |
| Tanoma: | Yarinyar da aka haifa lokacin ana noma. |
| Anaruwa | Yarinyar da aka haifa lokacin ana ruwa. |
| Mai goshi/Goshi | Yarinyar da aka haifa lokacin wadata. |
| Harende | Yarinyar da aka haifa a farkon wata |

**Auna fahimta na ɗaya (1)**

1. A waɗanne garuruwa ne ake samun sunayen Hausawa?
2. Kawo abubuwan da ake la'akari da su wajen sanya sunayen Hausawa.
3. Kawo sunayen lokaci na maza da mata uku-uku.

4. Cire bare ta fuskar jinsi daga cikin waɗannan sunaye.

i- Nomau
ii- Anaruwa
iii- Damina
iv- Marka

## 3.6 Sunayen Hausawa na Sanadin Haihuwa

Su kuma irin waɗannan sunayen Hausawa ana samu ne a ƙarƙashin wannan rukunin suna wanda yake samuwa a sakamakon afkuwar wani abu, kamar sanadiyar saki ko rigingimu a tsakanin ma'aurata da samun matsayi ko sarauta da mutuwa da sauransu, sai kawai a yi la'akari da sanadin a sanya wa jaririn wannan sunan. Ga misalan sunayen Hausawa na sanadi da ma'anarsu.

### 3.6.1 Sunayen Hausawa na sanadi na Maza.

Sunayen maza waɗanda ake yi la'akari da yanayin da aka haifi jaririn a sanya masa suna. Ga wasu sunayen maza na yanayi da ma'anarsu:

| SUNA | MA'ANA |
|---|---|
| Sadau/Dawaye/Dawai | Yaron da aka Haifa bayan mace ta bar gidan miji kuma ta koma |
| Hanau | Yaron da mace ta yi aure da nufin kome, sai aka sami ciki |
| Kamaye/Mayau | Yaron da aka Haifa bayan mutuwar ubansa |
| Audi | Yaron da ana haifarsa ubansa ya mutu |
| Gagarau/Gagar | Yaron da aka haife shi kakansa ya mutu |
| Korau/Magaji | Yaron ko yarinyan da aka Haifa a lokacin ganin sabon wata |
| Barau/Maraya/Talle/Tallafi | Yaron da uwarsa ta haife shi ta mutu |
| Kadarko | Yaron da aka haifa bayan aure uwarsa ya mutu, ta yi wani auren ta dawo |

| | |
|---|---|
| Shekarau/makau | Ɗa namiji wanda mahaifiyarsa ta ɗauki cikinsa tsawon shekara guda |
| Tanko/Mati/Mato/Namata/Guda/Gudaji/Kwalle | Yaron da ya biyo bayan haihuwar mata zalla |

### 3.6.2 Sunayen Hausawa na sanadi na mata.

Sunayen mata waɗanda ake yi amfani da yanayin da aka haifi jaririyar, a wajen sanya mata suna. Ga sunayen mata na lokaci da ma'anarsu:

| SUNA | MA'ANA |
|---|---|
| Guɗe | Yarinya da aka haifa bayan mace ta bar gidan miji kuma ta koma |
| Hanna | Yarinya da mace ta yi aure da nufin kome, sai aka sami ciki |
| Shekara | 'ya mace wanda mahaifiyarta ta ɗauki cikinta tsawon shekara guda. |
| Tune | Yarinya da mace ta yi aure da nufin kome, sai aka sami ciki |
| Sodangi/Sogiji | Yarinyar da aka haifa bayan iyayen sun yi ƙaura zuwa gida ko lokacin da aka taru don biki |
| Kilishi | Yarinyar da aka haifa a lokacin da mahaifinta ya sami sarauta ko wani matsayi |
| Bakuso | Yarinya da aka haifa bayan an rabu da uwarta |
| Rabo | Yarinyar da aka haifa bayan an sha rigingimu kafin auren |

## Auna fahimta na biyu (2)

| |
|---|
| 1. Waɗanne abubuwa ne suke samar da sunayen Hausawa na sanadi?<br>2. Kawo sunayen Hausawa maza na sanadi guda huɗu |

3. Kawo sunayen sanadi na Hausawa mata guda huɗu.
4. Mene ne sanadi sanya waɗannan sunaye a wajen Hausawa?
   i- Guda ii- Mati iii- Guda iv- Namata

## 3.7 Taƙaitawa

A taƙaice wannan kashin ya tattaro bayanai ne waɗanda suka danganci sunayen Hausawa da waɗanda suke samuwa a lokacin ruwa da sanyi ko hazo da sauransu da kuma ire-iren sunayen da ake samu a sanadiyyar wasu abubuwa kamar mutuwar 'ya'ya da rabuwar aure da rigingimu da sauransu. Sunayen Hausawa na lokaci da kuma na sanadi sun ƙunshi sunayen maza da mata.

## 3.8 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi

i- Kadarko - yaron da aka haifa bayan uwarsa ta fita ta yi wani aure ta dawo
ii- Kamaye - Yaron da aka Haifa bayan mutuwar ubansa
iii- Sodangi - Yarinyar da aka haifa bayan iyayen sun yi ƙaura zuwa gida ko lokacin
da aka taru don biki

## 3.9 Manazarta


Abdullahi I.S.S (2008). "Jiya ba Yau Ba: Waiwaye a Kan Al'adun Matakan Rayuwar

Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa." Kundin digiri na uku: Jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto.

Adamu, M. T. (2015). Tasirin Musulunci Kan Sunayen Hausawa. A Cikin *Harsunan Nijeriya*, Vol. XXV: 163-186.

Alhassan da Wasu (1987) *Zaman Hausawa.* Zaria: ABU Press.

Bichi A.Y (2013). *Tsokaci a Kan Bukukuwan Hausawa na Gargajiya wajen cigaban*

*Al'umma*. Zaria: Ahmadu Bello University, Press.

CNHN (1981). *Rayuwar Hausawa*. Lagos: Thomos Nilson Nigeria Limited.

Gusau, G.U (2012). *Bukukuwan Hausawa*. Gusau: Ol-Faith Prints

## 3.9 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahinta

Amsoshin Auna Fahinta na 1

1. A waɗanne garuruwa ne ake samun sunayen Hausawa?
   Amsa: -
   i- Arewancin Nijeriya
   ii- Jamhuriyar Nijar
   iii- Sudan
   iv- Ghana.

2. Kawo abubuwan da ake la'akari da su wajen sanya sunayen Hausawa.
   Amsa: -
   i- Lokaci
   ii- Sanadi
   iii- Siffa
   iv- Yanayi

3. Kawo sunayen lokaci na maza da mata uku-uku.

   Amsa: - **maza**
   i- Hantsi
   ii- Dare
   iii- Sammako
   iv- Magawata

   **mata**
   i- Harende
   ii- Marka
   iii- Tashuka
   iv- Baƙuwa

4. Cire bare ta fuskar jinsi daga cikin waɗannan sunaye.

   ii- Nomau
   iii- Anaruwa
   iv- Damina
   **v- Marka**

Amsoshin Auna Fahinta na 2

1- Waɗanne abubuwa ne suke samar da sunayen Hausawa na sanadi?
   Amsa: -
   i- sanadiyar saki
   ii- rigingimu a tsakanin ma'aurata

iii- samun matsayi ko sarauta
iv- mutuwa

2- Kawo sunayen Hausawa maza na sanadi guda huɗu.
Amsa: -

i- Kamaye
ii- Audi
iii- Gagarau
iv- Barau

3- Kawo sunayen sanadi na Hausawa mata guda huɗu.
Amsa: -
i- Guɗe
ii- Shekara
iii- Sodangi
iv- Kilishi

4- Mene ne sanadi sanya waɗannan sunaye a wajen Hausawa?
i- Guda ii- Mati iii- Guda iv- Namata
Amsa: - Sanadiyar mutuwar uwarsu bayan ta haife su.

## Kashi na Huɗu (4) Sunayen Hausawa na Gargajiya

### Abubuwan da Suke Ciki

4.1 Gabatarwa
4.2 Manufofi Darasi
4.3 Sunayen Hausawa na Yanayi
4.3.1 Sunayen Hausawa na Yanayi na maza
4.3.2 Sunayen Hausawa na yanayi na mata
4.4 Auna Fahinta
4.5 Sunayen Hausawa na Siffa
4.5.1 Sunayen Hausawa na Siffa na maza
4.5.2 Sunayen Hausawa na Siffa na mata
4.6 Taƙaitawa
4.7 Ma'anar Muhimman Kalmomi
4.8 Manazarta
4.9 Amsoshin Auna Fahimta

### 4.1 Gabatarwa

A cikin kashin da ya gabata, mun kawo bayanai kan sunayen da ake sanyawa 'ya'yan Hausawa waɗanda suka shafi gargajiyanci, wato sunaye na lokaci da sanadi. Amma a wannan darasin za mu yi bayani kan sunayen Hausawa na yanayi da na siffa, waɗanda ake amfani da su a sanadiyyar wasu abubuwa waɗanda suka haɗa da; haihuwar jarirai biyu da haihuwar ƙarshe da haihuwa bayan an haifi yara da yawa suna mutu, sannan da wanda aka haifa da yatsu fiye da biyar da zabiya ko fari ko ja da suaransu. Sunayen Hausawa na yanayi da na siffa sun ƙunshi na maza da mata.

### 4.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan rukuni ɗalibai za su iya:

- Bayani kan sunayen Hausawa na yanayi da na siffa.
- Zayyana sunayen Hausawa na yanayi na maza da na mata.
- Zayyana sunayen Hausawa na siffa na maza da na mata.
- Bayyana dalilan sanya sunayen Hausawa na yanayi da na siffa.

### 4.3 Sunayen Hausawa na Yanayin Haihuwa

A wannan nau'in sunayen Hausawa, ana la'akari da yanayin da haihuwar jariri ta kasance ko ta zo, kamar yaro ko yarinyar da aka haifa da riga ko yaran da ka haifa su biyu a lokaci guda da tagwaye mace da namiji da kuma wanda ko wadda aka haifa bayan an haifi 'yan biyu. Ire-

iren sunayen da ake samu a wannan fannin sun haɗa da na maza da na mata. Wasu daga sunayen da ake samu a wannan ɓangaren sun haɗa da: - Auwa da Ayashe da Kanta Shawai da sauransu.

### 4.3.1 Sunayen Hausawa na yanayi na Maza.

Sunayen maza waɗanda ake yi amfani da lokacin da aka haifi jaririn, a wajen sanya masa suna. Ga sunayen maza na lokaci da ma'anarsu:

| SUNA | MA'ANA |
|---|---|
| Mai riga | Yaron da aka haifa da tantanin haihu a lulluɓe |
| Yanbiyu/Tagwaye/ Biyu/ | Yaran da aka haifa su biyu a lokacin haihuwar |
| Leko/Gambo | Yaran da aka haifa bayan tagwaye maza ko mata |
| Kanta | Yaron da aka haifa tagwaye tare da mace |
| Tambai | Yaron da bora (matar da ba a so) ta haifa |
| Auta/Ɗan Auta | Yaron da aka fara haifa a ƙarshen haihuwa. |
| Anko | Yaron da aka haifa bayan mata. |

### 4.3.2 Sunayen Hausawa na yanayi na mata.

Sunayen maza waɗanda ake yi amfani da lokacin da aka haifi jaririn, a wajen sanya masa suna. Ga sunayen maza na lokaci da ma'anarsu:

| SUNA | MA'ANA |
|---|---|
| Mai riga/Ariguna/Sutura | Yaron da aka haifa da tantanin haihu a lulluɓe |
| Yanbiyu/Tagwaye/ Biyu/ | Yaran da aka haifa su biyu a lokacin haihuwar |
| Leko/Gambo | Yaran da aka haifa bayan tagwaye maza ko mata |
| Auwa | Yariyar da aka haifa |

| | |
|---|---|
| | tagwaye tare da namiji |
| Dela/Delu/Deluwa/Kande/Igge/Kyallu/Duwa | Yarinyar da aka haifa bayan maza |
| Ayashe/Ajuji/Ayas | Yarinyar da aka haifa bayan an yibta haihuwa suna mutuwa |
| Auta/’Yar Auta | Yaron da aka fara haifa a ƙarshen haihuwa. |
| Hakama/Gwamma | Yarinyar da aka haifa bayan an sa ran za a haifi namiji |
| Makwashi/Tambaya/Tambai/Xan Tambai | Yaron da bora (matar da ba a so) ta haifa |

## Auna fahimta na ɗaya (1)

1. Waɗanne abubuwa ne suke samar da sunayen Hausawa na yanayi?
2. Waɗanne abubuwa ne suke samar da sunayen Hausawa na yanayi?
3. Kawo sunayen Hausawa na yanayi na maza da na mata guda huɗu-huɗu
4. Kawo sunayen Hausawa na yanayi na maza da na mata guda huɗu-huɗu.

## 4.4 Sunayen Hausawa na Siffar Haihuwa

A wannan nau’in sunayen Hausawa, ana la’akari siffar da haifi jariri/jaririya da ita. Siffar za ta iya ƙunsar hasken jiki ko duhunsa da jan jiki ko ƙaramin jiki da sauransu. Ire-iren sunayen da ake samu a wannan fannin sun haɗa da na maza da na mata. Wasu daga sunayen da ake samu a wannan ɓangaren sun ƙunshi sunaye iren su, Cindo da Cibi da Wada da Zinaru da sauransu.

### 4.4.1 Sunayen Hausawa na maza na siffa.

Sunayen maza waɗanda suka shafi wannan rukuni ana amfani da irin siffar da aka haifi jariri da ita, a wajen sanya masa suna. Ga sunayen Hausawa maza na siffa da ma’anarsu:

| SUNA | MA'ANA |
|---|---|
| Cindo | Yaron da aka haifa da ƙarin ɗan yatsa na hannu ko na ƙafa |
| Wada | Yaron da aka haifa da ƙananan gaɓoɓi na hannu ko na ƙafa |
| Mai Cibi | Yaron da aka haifa da ƙatuwar cibiya |
| Jatau/Ɗan Ja | Yaron da aka haifa da farar fata |
| Duna | Yaron da aka haifa da siffar baƙi wuluk |
| Jinjiri | Yaron da aka haifa da ƙaramin jiki |
| Cira | Yaron da aka haifa da fata akan idonsa |

## 4.4.2 Sunayen Hausawa na yanayi na mata.

Sunayen mata waɗanda ake yi amfani da siffar da aka haifi jaririn da ita a wajen sanya masa suna. Ga sunayen mata na siffa da ma'anarsu:

| SUNA | MA'ANA |
|---|---|
| Kumatu | Yarinyar da aka haifa da manyan kumatu masu kauri |
| Cibi | Yarinyar da aka haifa da ƙatuwar cibiya |
| Zinaru/Faratu/'Yar Ja | Yarinyar da aka haifa da farar fata |
| Gudidi/Afiruwa/Jinjin/Jinjira/Kumbula/Jinjinniya | Yarinyar da aka haifa da ƙaramin jiki |
| Duduwa | Yarinyar da aka haifa baƙa wuluk |
| Buƙui | Yarinya da aka haifa da doro a baya kamar tozo |

| | |
|---|---|
| Tagatsori | Yarinya da aka haifa mai haƙora a waje |

**Auna fahimta na biyu (2)**

1. Waɗanne abubuwa ne suke samar da sunayen Hausawa na siffa?
2. Kawo sunayen Hausawa maza na siffa guda huɗu
3. Kawo sunayen siffa na Hausawa mata guda huɗu.
4. Wanne yanayi ne yake haifar da waɗannan sunaye a wajen Hausawa?
   i- Mai cibi ii- Cibi

## 4.5 Taƙaitawa

A taƙaice wannan kashin ya tattaro bayanai ne waɗanda suka danganci sunayen Hausawa na yanayi da na siffa. Sunayen Hausawa na yanayi da na siffa suna samuwa ne a snadiyyar wasu abubuwa kamar haifi jirirai biyu a lokaci guda da yaro/ yarinya da aka haifa a ƙarshe da haihuwa bayan an haifi yara da yawa suna mutu, sannan da wanda aka haifa da wata siffa kamar yatsu fiye da biyar a hannu ko a ƙafa da zabiya ko farin jariri ko jaririya da suaransu. Sai kuma aka kawo sunayen maza da na mata waɗanda suka shafi yanayi da siffa.

## 4.6 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi

- Cindo - Yaron da aka haifa da ƙarin ɗan yatsa na hannu ko na ƙafa
- Tozo – Wani irin tudu da ake samu a bayan raƙumi ko sa
- Tagatsori – suna ne da ake sa wa jariri wadda haƙorinta yake a waje.

## 4.7 Manazarta

Abdullahi I.S.S (2008). "Jiya ba Yau Ba: Waiwaye a Kan Al'adun Matakan Rayuwar

Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa." Kundin digiri na uku: Jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto.

Adamu, M. T. (2015). Tasirin Musulunci Kan Sunayen Hausawa. A Cikin *Harsunan Nijeriya*, Vol. XXV: 163-186.

Alhassan da Wasu (1987) *Zaman Hausawa.* Zaria: ABU Press.

Bichi A.Y (2013). *Tsokaci a Kan Bukukuwan Hausawa na Gargajiya wajen cigaban*

*Al'umma*. Zaria: Ahmadu Bello University, Press.

CNHN (1981). *Rayuwar Hausawa*. Lagos: Thomos Nilson Nigeria Limited.

Gusau, G.U (2012). *Bukukuwan Hausawa*. Gusau: Ol-Faith Prints.

## 4.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahinta

Auna fahinta ta farko (1)

1. Waɗanne abubuwa ne suke samar da sunayen Hausawa na yanayi?

Amsa: -

i- yaro ko yarinyar da aka haifa da riga
ii- yaran da ka haifa su biyu a lokaci guda
iii- yaron da aka haifa bayan tagwaye mace da namiji
iv- yaro/yarinyar da aka haifa bayan an haifi ‘yan biyu

2. Kawo sunayen Hausawa na yanayi na maza guda huɗu.
Amsa: -

i- Mairiga
ii- Biyu
iii- Ajuji
iv- Kanta
v- Ayashe da sauransu

3. Kawo sunayen Hausawa na yanayi na mata guda huɗu.

Amsa: -

i- Hakama
ii- ’Yar Auta
iii- ’Yan biyu
iv- Tambaya
v- Gambo da sauransu

4. Wane ne bare dangane da sunayen yanayi na Hausawa?

**a- Dela** b- Hakama c- Auta d- Ajuji

Auna fahinta ta biyu (2)

1. Waɗanne abubuwa ne suke samar da sunayen Hausawa na siffa?
Amsa: -
i- Hasken jiki
ii- duhun jiki
iii- jan jiki
iv- ƙaramin jiki

2. Kawo sunayen Hausawa na siffa na maza guda huɗu.

Amsa: - maza

i- Chido
ii- Wada
iii- Jatau
iv- Duna
v- Jinjiri da sauransu

3. Kawo sunayen Hausawa na siffa na mata guda huɗu.

Amsa: -mata

i- Kumatu
ii- Duduwa
iii- Cibi
iv- Tagatsori da sauransu

4. Wanne yanayi ne yake haifar da waɗannan sunaye a wajen Hausawa?

i- Mai cibi ii- Cibi

Amsa: - wanda/wadda aka haifa da ƙatuwar cibiya.

# RUKUNI NA BIYU (2)


| | |
|---|---|
| Kashi na Ɗaya (1) | Sunayen Hausawa Bayan Zuwan Musulunci |
| Kashi na Biyu (2) | Sunayen Ahalin Annabi Muhammad (SAW) |
| Kashi na Uku (3) | Sunayen Manyan Mata da Waliyyai |
| Kashi na Huɗu (4) | Wasu Sunayen Hausawa Bayan Zuwan Musulunci |


## Kashi na Ɗaya (1) Sunayen Hausawa Bayan Zuwan Musulunci

**Abubuwan da Suke Ciki**


1.1 Gabatarwa
1.2 Manufofi Darasi
1.3 Sunayen Hausawa Bayan Zuwan Musulunci
1.3.1 Hanyoyin Samun Sunayen Hausawa na Musulunci
1.3.2 Sunayen Hausawa Masu Sunan Allah
1.3.3 Sunayen Hausawa Masu Sunayen Annabawa
1.4 Taƙaitawa
1.5 Manazarta
1.6 Amsoshin Auna Fahimta


### 1.1 Gabatarwa

A cikin kashin da ya gabata, mun kawo bayanai kan sunayen da ake sanyawa ‘ya’yan Hausawa waɗanda suka shafi gargajiyanci, wato sunaye da suka shafi na siffa da na yanayi. Amma a wannan kashin za mu yi bayani kan sunayen Hausawa waɗanda suka shafi sunayen Hausawa bayan zuwan addinin musulunci wanda ya shafi sunayen Allah da na siffofinsa da kuma sunayen Annabawan Allah.


### 1.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan rukuni ɗalibai za su iya:

- Bayani kan sunayen Hausawa bayan zuwan musulunci.
- Zayyana Ire-Iren sunayen Hausawa bayan zuwan musulunci.
- Zayyana sunayen Hausawa masu sunan Allah.
- Sanin asalin wasu sunayen Allah da siffofinsa

## 1.3 Sunayen Hausawa Bayan Zuwan Musulunci

A wannan kashin akwai rukuni guda biyu, sunayen Hausawa wađanda ake amfani da su bisa la'akari da sunayen Allah da siffofinsa da Annabi Muhammad da na Annabawa da Mala'iku da na sahabban Annabi da sauransu. A ƙalla za a iya cewa sunayen Hausawa bayan zuwan musulunci sun kasu zuwa gida tara, kamar yadda Adamu (2015: 170). Ga wasu kađan a cikin tasawira:




**ZANE NA HUƊU**

Sai kuma wasu sunayen Hausawa na al'ada wađanda suke amfani da su wajen sanyawa 'ya'yansu bisa la'akari da ranaku da yanayi da kuma lokaci da aka haifi jariri/jaririyar.

Sai kuma wađanda suke amfani da su bisa sha'awa ko ra'ayi ko kuma wata soyayya ta musamman, kamar haka:




### 1.3.1 Hanyoyin da Ake Samun Sunayen Hausawa Bayan Zuwan Musulunci

Akwai hanyoyin da Hausawa suke amfani da su samawa 'ya'yansu suna bayan zuwan musulunci ƙasar Hausa. Hanyoyin sun haɗa da: -

i- Littafin Alƙur'ani mai tsarki
ii- Hadisai na Annabi (SAW)
iii- Sauran littattafan musulunci

### 1.3.2 Sunayen Hausawa Masu Sunan Allah

Akwai sunayen masu nuna siffofin Allah Ubangiji Maɗaukacin sarki masu yawa, don haka al'ummar Hausawa suna ɗaya daga cikin rukunin mutanen da suke amfani da irin waɗannan sunaye wajen sanya wa 'ya'yansu tare da raɓa sunan Abdul a kan sunan da sauransu. A sunayen Allah babu wani suna da Hausawa suke amfani da shi ga 'ya'yansu mata.

Misali

| SUNAN ALLAH | SUNAYEN HAUSAWA |
|---|---|
| Abdulrazzaƙi | Abdulrazaƙu |
| Abdulsalam | Abdulsalamu |
| Abdulrahaman | Abdulrahamanu |
| AbdulAziz | Abdul'Azizu |

| | |
|---|---|
| AbdulJabbar | Abduljabbaru |
| Abdulsamad | Abdulsamad |
| Abdulwahab | Abdulhabu |

### 1.3.3 Sunayen Hausawa Masu Sunayen Annabawa

A cikin tsarin sunayen da Hausawa suke amfani da shi, akwai sunayen Annabawa da yawa da Hausawa suke amfani da su wajen sanyawa 'ya'yansu duk da cewa akwai wata 'yar kwaskwarima da suke yi wa sunayen, misalai:

| Asalin suna | Yadda Hausawa ke amfani da shi |
|---|---|
| Annabi Adam (AS) | Ado/ Ada/ Adamu |
| Annabi Saleh (AS) | Saluhu/Sale/ Salele |
| Annabi Ibrahim (AS) | Ibro/Khalili/ Iro /Barhama |
| Annabi Yunus (AS) | Inusa/ Nusa/ Yunusa |
| Annabi Musa (AS) | Kalla/Kallamuda/ Musalle |
| Annabi Yusuf (AS) | Isuhu/Yusufa/Isuhulle |
| Annabi Sulaiman (AS) | Sule/Ɗandauda/Sulaiman |
| Annabi Muhammada (SAW) | Mamman/Mammalo/Madu/Mado, Inuwa/ Manzo/ Na-Allah |

**Auna fahimta ta farko (1)**

1- Gida nawa sunayen Hausawa bayan zuwan musulunci suka kasu?
2- Kawo sunayen Hausawa masu ɗauke da siffofin Allah guda huɗu
3- Kawo sunayen Hausawa masu ɗauke da sunan Annabawa guda huɗu.
4- Kawo misalai biyar na sunayen da Hausawa suka ƙirƙira daga sunayen Annabawa.

## 1.4 Sunayen Annabi Muhammad (SAW)

Ƙarƙashin wannan akwai ɓangarori guda biyu, akwai sunayen Annabi Muhammad (SAW) waɗanda shafi ƙidaya da kuma halayen Annabi Muhammad (SAW). Hausawa suna amfani da irin waɗannan sunaye wajen sanya wa 'ya'yansu.

### 1.4.1 Sunayen Annabi Muhammad (SAW) na Ƙidaya

Akwai sunayen Annabi na ƙidaya waɗanda suka fara daga ɗaya zuwa goma. Al'ummar Hausawa suna ɗaya daga cikin rukunin mutanen da suke amfani da irin waɗannan sunaye wajen sanya wa 'ya'yansu, misali:

| SUNAN | SUNAYEN HAUSAWA |
|---|---|
| Muhammad Auwal na 1 | Auwalu/ Lawan/Lawwali/Lawai/Lawandi |
| Muhammad Sani na 2 | Sani/Sanini |
| Muhammad Salisu na 3 | Salisu |
| Muhammad Rabi'u na 4 | Rabi'u/ Rabe/ Rabebe |
| Muhammad Khamis na 5 | Hamisu/ Hami |
| Muhammad Sadis na 6 | Sadisu/ Sadi |
| Muhammad Sabi'u na 7 | Sabi'u/Sabi |
| Muhammad Saminu na 8 | Saminu/ Sami |
| Muhammad Tasi'u na 9 | Tasi'u/ Tasi |
| Muhammad Ashir na 10 | Ashiru/ Nagoma |

### 1.4.2 Sunayen Annabi Muhammad (SAW) na Hali

A cikin tsarin sunayen da Hausawa suke amfani da su, akwai sunayen Annabi Muhammad (SAW) da yawa. Hausawa suna amfani da sunayen masu bayyana halayen Annabi Muhammad (SAW) wajen sanyawa 'ya'yansu, misalai:

| **Asalin suna** | **Yadda Hausawa ke amfani da shi** |
|---|---|
| Amin | Aminu |
| Ɗaha | Ɗahe/Tsahe |
| Habib | Habibu |
| Shakur | Shakuru |
| Wakil | Wakili |
| Hamid | Hamidu/Hamidan |

| | |
|---|---|
| Kamil | Kamulu/Kamilalle |
| Mansur | Mansir |
| Misbah | Musbahu |
| Suraj | Surajo |

**Auna fahimta ta biyu (2)**

1- Sunaye Annabi Muhammad (SAW) sun kasu gida__________
2- Kawo sunayen Annabi Muhammad (SAW) na ƙidaya guda huɗu
3- Kawo sunayen Annabi Muhammad (SAW) na hali guda huɗu.
4- Cire bare dangane sunayen Annabi na ƙidaya.
a- Sani b- Salisu c- Kamil d- Ashiru

## 1.5 Taƙaitawa

A taƙaice wannan kashin ya tattaro bayanai ne waɗanda suka danganci sunayen Allah da siffofinsa da kuma sunayen Annabawa waɗanda Hausawa suka yi wa wasu daga ciki 'yar kwaskwarima, suke sanya wa 'ya'yansu da aka haifa. A kashin an kawo sunayen Allah da kuma sunaye na Annabawan Allah.

## 1.6 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi

Amin – mai gaskiya
Habib – masoyi ko abun so
Musbahu – haske
Nur - haske
Mubasshir – mai bushara

## 1.7 Manazarta

Abdullahi I.S.S (2008). "Jiya ba Yau Ba: Waiwaye a Kan Al'adun Matakan Rayuwar

Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa." Kundin digiri na uku: Jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto.

Adamu, M. T. (2015). Tasirin Musulunci Kan Sunayen Hausawa. A Cikin *Harsunan Nijeriya*, Vol. XXV: 163-186.

Alhassan da Wasu (1987) *Zaman Hausawa.* Zaria: ABU Press.

Bichi A.Y (2013). *Tsokaci a Kan Bukukuwan Hausawa na Gargajiya wajen cigaban Al'umma*. Zaria: Ahmadu Bello University, Press.

CNHN (1981). *Rayuwar Hausawa*. Lagos: Thomos Nilson Nigeria Limited.

Gusau, G.U (2012). *Bukukuwan Hausawa*. Gusau: Ol-Faith Prints.

## 1.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

Auna fahinta ta farko (1)

1- Gida nawa sunayen Hausawa bayan zuwan musulunci suka kasu?
Amsa:- tara

2- Kawo sunayen Hausawa masu ɗauke da siffofin Allah guda huɗu.
Amsa: -
i- Abdulrazzaƙ
ii- Abdulrahaman
iii- Abdulaziz
iv- Abdulsalam
v- Abduljabbar da sauransu

3- Kawo sunayen Hausawa masu ɗauke da sunan Annabawa guda huɗu.
Amsa: -
i- Adamu
ii- Musa
iii- Ayuba
iv- Dauda
v- Isa da sauransu

4- Kawo misalai biyar na sunayen da Hausawa suka ƙirƙira daga sunayen Annabawa.

Amsa: -

i- Ado
ii- Inusa
iii- Isuhu
iv- Mamman
v- Salele da sauransu

Auna fahinta ta biyu (2)

1- Sunaye Annabi Muhammad (SAW) sun kasu gida__________
Amsa: - biyu

2- Kawo sunayen Annabi Muhammad (SAW) na ƙidaya guda huɗu.
Amsa: -

i- Auwalu
ii- Sani
iii- Salisu

iv- Salihu
v- Kamisu
vi- Sadisu da sauransu
3- Kawo sunayen Annabi Muhammad (SAW) na hali guda huɗu.

Amsa: -

i- Amin
ii- Sadiƙ
iii- Habib
iv- Ɗaha
v- Wakil da sauransu
4- Cire bare dangane sunayen Annabi na ƙidaya.
Sani b- Salisu **c- Kamil** d- Ashiru

## Kashi na Biyu (2) Sunayen Ahalin Annabi Muhammad (SAW)

**Abubuwan da Suke Ciki**

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufofi Darasi
2.3 Sunayen Ahalin Annabi Muhammad (SAW)
2.3.1 Sunayen Matan Annabi
2.3.2 Sunayen ‘Yayan Annabi
2.4 Taƙaitawa
2.5 Manazarta
2.6 Amsoshin Auna Fahimta

### 2.1 Gabatarwa

A cikin rukunin da ya gabata, mun kawo bayanai kan sunayen da Hausawa suke sanyawa ‘ya’yan waɗanda suka shafi addini, wato sunayen Ahalin Annabi Muhammad (SAW). Amma a wannan darasin za mu yi bayani kan sunayen Hausawa waɗanda suka shafar sunayen Alhalin Annabi Muhammad (SAW). Sunayen sun haɗa da na matan Annabi da kuma na ‘ya’yansa.

### 2.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan rukuni ɗalibai za su iya:

- Bayani kan sunayen Ahlin Gidan Annabi Muhammad SAW) da Hausawa ke amfani
  da su.
- Zayyana Ire-Iren sunayen Matan Annabi Muhammad (SAW) da Hausawa ke amfani
  da su.
- Zayyana sunayen ‘Yayan Annabi Muhammad (SAW) da Hausawa ke amfani
  da su.
- Bambance sunayen Matan Annabi da ‘Yayansa.

### 2.3 Sunayen Ahalin Annabi Muhammad (SAW)

Ƙarƙashin wannan akwai ɓangarori guda biyu, akwai ɓangaren sunayen Matan Annabi Muhammad (SAW) da kuma na ‘Ya’yansa. Hausawa suna amfani da ire-iren waɗannan sunaye wajen sanya wa ‘ya’yansu.

## 2.3.1 Sunayen Matan Annabi Muhammad (SAW)

Akwai sunayen Matan Annabi guda goma sha ɗaya. Al'ummar Hausawa suna ɗaya daga cikin rukunin mutanen da suke amfani da irin waɗannan sunaye wajen sanya wa 'ya'yansu, misali:

| SUNAN ASALI | SUNAYEN HAUSAWA |
|---|---|
| Nana Khadija | Hadiza/Kubura/Dije/Dijangala |
| Nana Saude | Saude/Sauda |
| Nana A'isha | A'i/Aisha/Indo/Shatu/A'ilo |
| Nana Hafsah | Hafsatu/Hausat/Hansai |
| Nana Zainab | Zainaba/Abu/Abuwa/Buwalle/Abulle |
| Nana Maimuna | Maimuna/Munari/Munai/Minu |
| Nana Juwairiyya | Zuwaira/Zuwaire/Zuwai |
| Nana Ramlah | Ramratu/Ramala/Hindede |
| Nana Safiyya | Safiya/Safi |
| Nana Mariya | Mariya/Mari |

## 2.3.2 Sunayen 'Ya'yan Annabi Muhammad (SAW)

A cikin tsarin sunayen da Hausawa suke amfani da su, akwai sunayen 'Ya'yan Annabi Muhammad (SAW) da yawa. Hausawa suna amfani da sunayen masu 'Ya'yan Annabi Muhammad (SAW) wajen sanyawa 'ya'yansu, misalai:

| **Asalin suna** | **Yadda Hausawa ke amfani da shi** |
|---|---|
| Alƙassim | Ƙasimu/Alkakasim/Alka |
| Abdullahi | Audullahi/Abdallah |
| Ibrahim | Mu'azzam/Mu'azzamu/Iro |
| Zainab | Zainaba/Abu/Abuwa/Abulle |
| Ruƙayya | Rakiya/Ruƙai/Raki |
| Ummukulsum | Kattume/Ummakati |
| Fatima | Batulu/Zahra'u/Zara/Tarasulu/Ta'Annabi |

**AUNA FAHIMTA TA FARKO (1)**

1- Sunayen da hausawa suke amfani da shi na Ahlin Gidan Annabi Muhammad (SAW) sun kasu gida__________
2- Kawo sunayen Matan Annabi Muhammad (SAW) guda huɗu
3- Kawo sunayen 'Yayan Annabi Muhammad (SAW) guda huɗu.
4- Cire bare dangane rukunin sunayen Hausawa.
a- Ruƙayya b- Juwairiyya c- Mariya d- Safiya

## 2.4 Sunayen Sahabban Annabi Muhammad (SAW)

Sahabbai su ne mutane maza da mata waɗanda suka ga Annabi (SAW) kuma suka yi imani da abun da ya zo da shi, suka kuma taimaka masa wajen isar da saƙon da ya zo da shi. da Ƙarƙashin wannan akwai ɓangarori guda biyu, akwai ɓangaren sunayen Sahabban Annabi Muhammad (SAW) maza da kuma na Sahabbai mata. Hausawa suna amfani da ire-iren waɗannan sunaye wajen sanya wa 'ya'yansu.

### 2.4.1 Sunayen Sahabban Annabi Muhammad (SAW) maza

Akwai sunayen Sahabban Annabi maza da mata. Al'ummar Hausawa suna ɗaya daga cikin rukunin mutanen da suke amfani da irin waɗannan sunaye wajen sanya wa 'ya'yansu, misali:

| SUNAN | SUNAYEN HAUSAWA |
|---|---|
| Abubakar Bin Saddiƙu | Hadiza/Kubura/Dije/Dijangala |
| Umar Bin Khattab | Umari/Umara/Umarere/Sanda/Faruƙ |
| Usman Bin Affan | Usman/Usma/Shehu |
| Aliyu Bin Abi Talib | Ali/Gadanga/Zaki |
| Talha Bin Ubaidullah | Tsalha/Ɗalha |
| Zubair Bin Auwam | Zubairu |
| Abdul Rahaman Bin Auf | Bin Auf |
| Sa'ad Bin Abi Waƙƙas | Sa'adu |
| Sa'id Bin Zaid | Sa'idu |
| Abu Ubaidah Bin Jarrah | Abu Ubaidata |

### 2.4.2 Sunayen Sahabban Annabi Muhammad (SAW) Mata

A cikin tsarin sunayen da Hausawa suke amfani da su, na yau da kullum akwai sunayen Sahabban Annabi Muhammad (SAW) waɗanda mata ne. Hausawa suna amfani ire-iren sunayen Sahabbai a wajen sanya wa 'ya'yansu, misalai:

| Asalin suna | Yadda Hausawa ke amfani da shi |
|---|---|
| Aliyah | Aliya |
| Asma | Asma'u |
| Huraira | Furaira |
| Karimah | Karimatu |
| Rumaisa | Rumasa'u/Ruma |
| Rahanah | Rahanatu |
| Nafisah | Nafisa/Nafi/Nafisatu |
| Lubaba | Lubabatu/Lube/Luba |
| Su'adah | Sa'adatu/Sa'a/Sa'ade |

**Auna fahimta ta biyu (2)**

1- Sunaye Hausawa na Sahabbai gida__________
2- Kawo sunayen Hausawa na Sahabbai maza guda huɗu.
3- Kawo sunayen Hausawa na Sahabbai mata guda huɗu.
4- Cire bare dangane sunayen Hausawa na mata.
a- Rufaida b- Su'adah c- Safwan d- Lube

## 2.5 Taƙaitawa

A wannan kashin, mun yi bayani kan sunayen Matan Annabi Muhammad (SAW) da kuma na 'ya'yansa. Sannan mun kawo yadda Hausawa suke amfani da sunayen wajen sanya wa 'ya'yansu. Kuma mun kawo misalai a kowane ɓangare na sunayen.

## 2.6 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi

Bin- ɗa
Rumaisa – sunan mace
Huraira – sunan mace
Ubaidah – sunan namiji

## 2.7 Manazarta

Abdullahi I.S.S (2008). "Jiya ba Yau Ba: Waiwaye a Kan Al'adun Matakan Rayuwar

Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa." Kundin digiri na uku: Jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto.

Adamu, M. T. (2015). Tasirin Musulunci Kan Sunayen Hausawa. A Cikin *Harsunan Nijeriya,* Vol. XXV: 163-186.

Alhassan da Wasu (1987) *Zaman Hausawa.* Zaria: ABU Press.

Bichi A.Y (2013). *Tsokaci a Kan Bukukuwan Hausawa na Gargajiya wajen cigaban Al'umma*. Zaria: Ahmadu Bello University, Press.

CNHN (1981). *Rayuwar Hausawa*. Lagos: Thomos Nilson Nigeria Limited.

Gusau, G.U (2012). *Bukukuwan Hausawa*. Gusau: Ol-Faith Prints.

## 2.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

Auna fahimta ta farko (1)

1- Sunayen da hausawa suke amfani da shi na Ahlin Gidan Annabi Muhammad (SAW) sun kasu gida__________

Amsa: - biyu

2- Kawo sunayen Matan Annabi Muhammad (SAW) guda huɗu.

Amsa: -

i- Aisha
ii- Khadija/Hadiza
iii- Safiya
iv- Zainab
v- Mariya da sauransu

3- Kawo sunayen ‘Yayan Annabi Muhammad (SAW) guda huɗu.

Amsa: -

i- Ibrahim
ii- Zainab
iii- Ruƙayya
iv- Fatima
v- Ruƙayya da sauransu

Cire bare dangane rukunin sunayen Hausawa

a- **Ruƙayya** b- Juwairiyya c- Mariya d- Safiya

Auna fahimta ta biyu (2)

1- Sunaye Hausawa na Sahabbai gida__________
Amsa: - biyu

2- Kawo sunayen Hausawa na Sahabbai maza guda huɗu.
Amsa: -

i- Abubakar
ii- Umar
iii- Usman
iv- Aliyu
v- Ɗalha
vi- Zubair da sauransu

3- Kawo sunayen Hausawa na Sahabbai mata guda huɗu.

Amsa: -

i- Nafisa
ii- Ruhana
iii- Lubabatu
iv- Karima
v- Huraira da sauransu.

4- Cire bare dangane sunayen Hausawa na mata.

a- Su'adah b- Ado c- sale d- Lube

## Kashi na Uku (3) Sunayen Manyan Mata da Waliyyai

### Abubuwan da Suke Ciki

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufofi Darasi
3.3 Sunayen Manyan Bayin Allah
3.3.1 Sunayen Manyan Mata
3.3.2 Sunayen Waliyyai
3.4 Taƙaitawa
3.5 Manazarta
3.6 Amsoshin Auna Fahimta

## 3.1 Gabatarwa

A cikin wannan kashin, mun gabatar da bayanai kan sunayen da Hausawa suke sanyawa 'ya'yansu, suanyen sun samu ne bayan zuwan musulunci, wato sunaye ne na Sahabban Annabi Muhammad (SAW) waɗanda Hausawa suka yi masu 'yar kwaskwarima suke amfani da su a cikin harshen Hausa. Amma a wannan darasin za mu yi bayani ne kan sunayen da Hausawa suke sanya wa 'ya'yansu waɗanda suka shafi sunayen Manyan Mata na duniya da Waliyyai.

## 3.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan rukuni ɗalibai za su iya:

- Bayani kan sunayen Waliyyan Allah.
- Zayyana Ire-Iren sunayen Waliyyai Maza.
- Zayyana wasu sunayen Waliyyai mata
- Bambace sunayen Waliyyai Mata da Maza.

## 3.3 Sunayen Waliyyai Allah

Sunayen manyan bayin Allah suna ne wanda ya ƙunshi sunayen matayen Annabawa da maihaifansu da kuma sunayen waɗanda suka yi rainon wasu Annabawa, da kuma sauran Waliyyai kamar Halimatu Sadiya wadda ita ce ta yi rainon Annabi Muhammada (SAW) sai Nana Asiya wadda ta yi rainon Annabi Musa (AS). Waliyyai wasu mutane ne masu tsoron Allah da yin biyayya gare shi a fili da ɓoye, waɗanda Allah ya yarda da su. Ƙarƙashin wannan akwai ɓangarori guda biyu, akwai ɓangaren sunayen Manyan Mata da Waliyyai Maza. Hausawa suna amfani da ire-iren waɗannan sunaye wajen sanya wa 'ya'yansu.

**Auna fahimta ta farko (1)**

| |
|---|
| 1- Su waye manyan bayin Allah mata?<br>2- Kawo sunayen da Hausawa suka yi amfani na Waliyyai Mata guda biyu.<br>3- Me kalmar Waliyya take nufi?<br>4- Cire bare dangane sunayen Hausawa na masu Raino.<br>a- Nana Asiya b- Halima c- Sadiya d- Bilki |

## 3.3.1 Sunayen Waliyyai Mata

Akwai sunayen bayin Allah na mata kuma al'ummar Hausawa suna ɗaya daga cikin rukunin mutanen da suke amfani da irin waɗannan sunaye wajen sanya wa 'ya'yansu domin neman 'ya'yansu albarka, misali:

| SUNAN | SUNAYEN HAUSAWA |
|---|---|
| Nana Hauwa'u matar Annabi Adam (AS) | Hauwa/Kulu/Maijidda/Jidda/Kuluwa |
| Nana Amina mahaifiyar Annabi (SAW) | Amina/Gwarje/ Ami/Burungu/Mina |
| Nana Maryam mahaifiyar Annabi Isa (AS) | Maryama/Daso/Mairo |
| Nana Hajara matar Annabi Ibrahim (AS) | Hajara/Hajo/Aya/Ayar Allah |
| Nana Saratu matar Annabi Adam (AS) | Saratu/Sarai/Tatu |
| Nana Rahmatu matar Annabi Ayuba (AS) | Ramatu/Ramai |
| Nana Asiya matar Fir'auna | Hasiya/Hasi |
| Nana Zulaiha matar Annabi Yusuf (AS) | Zilai/Zilaihatu/zaliyya |
| Nana Bilkisu matar Annabi Sulaiman (AS) | Bulki/Bilkisu/Maigadon/Kisu/Gado |
| Nana Halimatul Sa'adiyya mai renon Annabi (SAW) | Dubu/Sadiya/Hali/Matu |

### 3.3.2 Sunayen Waliyyai Maza

A cikin tsarin sunayen da Hausawa suke amfani da su na yau da kullum akwai sunayen Waliyyai waɗanda suka ƙunshi sunayen maza. Hausawa suna amfani ire-iren sunayen Waliyyai aas wajen sanya wa 'ya'yansu, misalai:

| **Asalin suna** | **Yadda Hausawa ke amfani da shi** |
|---|---|
| Abu Hanifa (imam) | Hannafi/Hanifa |
| Badawi (Shehu Ahmad) | Badawi/Badayi |
| Baihaƙi (Imam Ahmad Bin Hussain) | Baihaƙi |
| Bukhari (Imam Muhd. Bn Isma'il) | Buhari |
| Malik (Imam Malik) | Maliku/Maliki |
| Junaid ( Shehu Abul Ƙasim) | Junaidu |
| Garzali (Imam Abi Hamid) | Garzali |
| Muslim (Imam Abil Hussain Bin Hajjaj) | Musulumu |
| Turmmizi (Imam Abu Isa Muhd. Albugiy | Turmuzi |

### Auna fahimta ta biyu (2)

1- Sunaye Hausawa na Waliyyai ya kasu gida__________
2- Kawo sunayen Hausawa na Waliyyai Mata guda huɗu.
3- Kawo sunayen Hausawa na Waliyya Maza guda huɗu.
4- Cire bare dangane sunayen Hausawa na Bilkis.
b- Bilkisub- Bulki c- Dubu d- Gado

### 3.4 Taƙaitawa

A wannan kashin, mun yi bayani kan sunayen Waliyyan Allah waɗanda Hausawa suke amfani da su wajen sanya wa 'ya'yansu. Sannan mun kawo sunayen Waliyyai maza da na mata. A ƙarshe, mun nuna kwaskwarimar da Hausawa suke yi wa wasu sunayen a cikin misalai:

## 3.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi

Nana Amina – ita ce mahafiya ga Annabi Muhammad (SAW)
Nana Maryam - ita ce mahaifiyar Annabi Isa Alaishi Salam
Nana Asiya – ita ce yi renon Annabi Musa
Dubu – suna ne da ake yi mace mai suna Halima (hali dubu babu na yarwa.

## 3.6 Manazarta

Abdullahi I.S.S (2008). "Jiya ba Yau Ba: Waiwaye a Kan Al'adun Matakan Rayuwar

Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa." Kundin digiri na uku: Jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto.

Adamu, M. T. (2015). Tasirin Musulunci Kan Sunayen Hausawa. A Cikin *Harsunan Nijeriya*, Vol. XXV: 163-186.

Alhassan da Wasu (1987) *Zaman Hausawa.* Zaria: ABU Press.

Bichi A.Y (2013). *Tsokaci a Kan Bukukuwan Hausawa na Gargajiya wajen cigaban Al'umma*. Zaria: Ahmadu Bello University, Press.

CNHN (1981). *Rayuwar Hausawa*. Lagos: Thomos Nilson Nigeria Limited.

Gusau, G.U (2012). *Bukukuwan Hausawa*. Gusau: Ol-Faith Prints.

## 3. 7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

Auna fahimta ta farko (1)

1- Su waye manyan bayin Allah mata?
Amsa: -
Suna ne matayen Annabawa da maihaifansu da kuma sunayen waɗanda suka yi rainon wasu Annabawa, da kuma sauran Waliyyai

2- Kawo sunayen da Hausawa suka yi amfani na Waliyyai Mata guda biyu.

Amsa: -
i- Nana Hasiya
ii- Nana Halimatul Sadiya

3- Me kalmar Waliyya take nufi?
Amsa: -

Waliyyai wasu mutane ne masu tsoron Allah da yin biyayya gare shi a fili da ɓoye, waɗanda Allah ya yarda da su.

4- Cire bare dangane sunayen Hausawa na masu Raino.
**a-** Nana Asiya b- Halima c- Sadiya d- **Bilki**

Auna fahimta ta biyu (2)

1- Sunaye Hausawa na Waliyyai ya kasu gida__________
Amsa: - biyu

2- Kawo sunayen Hausawa na Waliyyai Mata guda huɗu.
Amsa: -
i- Nana Hawwa'u
ii- Nana Hajara
iii- Nana Amina
iv- Nana Asiya
v- Nana Halima da sauransu

3- Kawo sunayen Hausawa na Waliyya Maza guda huɗu.
Amsa: -

i- Imam Garzali
ii- Imam Muslim
iii- Imam Bukhari
iv- Imam Abu Hannifa
v- Imam Malik da sauransu.

4- Cire bare dangane sunayen Hausawa na Bilkis.
a- Bilkisu b- Bulki **c- Dubu** d- Gado

# Kashi na Huɗu (4) Wasu Sunayen Hausawa Bayan Zuwan Musulunci

**Abubuwan da Suke Ciki**

4.1 Gabatarwa
4.2 Manufofi Darasi
4.3 Wasu Sunayen Hausawa Bayan Zuwan Musulunci
4.3.1 Sunayen Mala'iku
4.3.2 Sunayen daga Ayoyi da Surori na Alƙur'ani
4.4 Taƙaitawa
4.5 Manazarta
4.6 Amsoshin Auna Fahimta

## 4.1 Gabatarwa

A cikin wannan kashin, mun gabatar da bayanai kan sunayen da Hausawa suke sanyawa 'ya'yansu, sunayen sun samu ne bayan zuwan musulunci, wato sunaye ne waɗanda suka shafi Waliyyai Maza da Mata. Hausawa sukan yi wa wasu sunayen wata 'yar kwaskwarima a cikin harshen Hausa. Amma a wannan darasin za mu yi bayani ne kan sunayen da Hausawa suke sanya wa 'ya'yansu waɗanda suka shafi sunayen Mala'iku da na ayoyi da kuma surori na Alƙur'ani.

## 4.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan rukuni ɗalibai za su iya:

- Bayani kan sunayen Mala'ikun Allah.
- Zayyana Ire-Iren sunayen Mala'iku.
- Zayyana wasu sunayen Ayoyi na Alƙur'ani
- Kawo sunayen Surori na Alƙur'ani.

## 4.3 Sunayen Hausawa Bayan Zuwan Musulunci

sunayen da Hausawa suke amfani da su a wannan fannin sun samu ne bayan zuwan musulunci, wato sunaye ne waɗanda suka shafi Mala'iku da kuma na ayoyi da surori waɗanda aka samo daga cikin Alƙur'ani mai girma. Hausawa suka yi masu wata 'yar kwaskwarima a cikin harshen Hausa.

### 4.3.1 Sunayen Mala'iku

Mala'iku wata halitta ce da Allah ya yi daga haske wadda take da tsananin biyayya ga umarninsa (Ƙamusun Hausa, 2006: 327). Akwai

sunayen Mala'iku waɗanda al'ummar Hausawa na ɗaya daga cikin rukunin mutanen da suke amfani da irin waɗannan sunaye wajen sanya wa 'ya'yansu domin nema wa 'ya'yansu albarka. Sunayen wasu daga Mala'ikun ya haɗa da:

| SUNAN | SUNAYEN HAUSAWA |
|---|---|
| Jibril | Jibir/Jibbo/Jibrin |
| Mika'il | Mika'ilu/Miko/Kaila/Mika |
| Malik | Maliku/Maliki |
| Ridwan | Lurwanu |

**Auna fahimta ta farko (1)**

1- Su waye Mala'iku?
2- Kawo sunayen da Hausawa suke amfani da su na Mala'iku guda huɗu.
3- Sunan Jibbo daidai yake da sunan _______
4- Cire bare daga waɗannan sunayen Hausawa.
a- Maliku b- Jibrin c- Malik d- Izazul

## 4.3.2 Sunayen Ayoyi da Surori

A cikin tsarin sunayen da Hausawa suke amfani da su na yau da kullum akwai sunayen Ayoyi da surori. Hausawa suna amfani da sunayen da suka samo daga cikin Alƙur'ani mai girma, sai duba kan wata aya ko sura da ta yi musu daɗi sai su sanya 'ya'yansu, ko da kuwa ma'anar sunan abu ne masas kyau, su babu ruwansu. Alƙur'ani suke kallo kawai ba ma'anar ba, kuma mafi yawan irin waɗannan sunaye an fi sanya wa 'ya'ya mata (Adamu, 2015180). Misali:

| Asalin suna | Yadda Hausawa ke amfani da shi |
|---|---|
| Lantana (cikin Sura ta 3 aya ta 92) | Lantana |
| Ƙalafama ( cikin Sura ta 51 aya ta 31) | Kalafa |
| Izawaƙa (cikin Sura ta 56 aya ta 1) | Izawaƙa |
| Tabara (cikin Sura ta 67 aya ta 1) | Tabara |
| Alhaƙƙatu (cikin Sura ta 69 aya ta 1) | Alhaƙatu |
| Ƙuluhiya (cikin Sura ta 73 aya ta 1) | Kulubiya |

| | |
|---|---|
| Abasa (cikin Sura ta 80 aya ta 1) | Abasa |
| Bara’atu (cikin Sura ta  aya ta ) | Bara’atu |
| Shafa’atu (cikin Sura ta  aya ta ) | Shafa’atu |

**Auna fahimta ta biyu (2)**

| | |
|---|---|
| 1. | Akwai sunaye na ayoyi da ________ da Hausawa suke amfani da su. |
| 2. | Kawo sunayen da Hausawa suke amfani da su na ayoyi guda uku. |
| 3. | Kawo sunayen surori guda uku da Hausawa suke amfani da su. |
| 4. | Cire bare daga cikin waɗannan sunayen Hausawa. |
| a- | Maliku b-  Bara’atu c- Abasa  d- Ƙuluhiya. |

## 4.5 Taƙaitawa

A wannan kashin, mun yi bayani kan sunayen Mala’iku da na ayoyi da na surori waɗanda Hausawa suke amfani da su wajen sanya wa ‘ya’yansu. A ƙarshe mun nuna yadda Hausawa suke yi wa wasu sunayen Mala’iku da ayoyi da na surori kwaskwarima.

## 4.6 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi

Jibril -
Mika’il -
Malik –
Ridwan –
Abasa –
Lantana -
Ƙuluhiya -

## 4.7 Manazarta

Abdullahi I.S.S (2008). “Jiya ba Yau Ba: Waiwaye a Kan Al’adun Matakan Rayuwar

Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa.” Kundin digiri na uku: Jami’ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto.

Alhassan da Wasu (1987) *Zaman Hausawa.* Zaria: ABU Press.

Bichi A.Y (2013). *Tsokaci a Kan Bukukuwan Hausawa na Gargajiya wajen cigaban Al’umma*. Zaria: Ahmadu Bello University, Press.

CNHN (1981). *Rayuwar Hausawa*. Lagos: Thomos Nilson Nigeria Limited.

Gusau, G.U (2012). *Bukukuwan Hausawa*. Gusau: Ol-Faith Prints.

## 1.6 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

**Auna fahimta ta farko (1)**

1- Su waye Mala'iku?
Amsa: -

Mala'iku wata halitta ce da Allah ya yi daga haske wadda take da tsananin biyayya ga umarninsa (Ƙamusun Hausa, 2006: 327).

2- Kawo sunayen da Hausawa suke amfani da su na Mala'iku guda huɗu.
Amsa: -

i- Jibril
ii- Malik
iii- Mika'il
iv- Ridwan

3- Sunan Jibbo daidai yake da sunan _______
Amsa: - Jibrin

4- Cire bare daga waɗannan sunayen Hausawa.

Maliku b- Jibrin c- Malik d- **Izazul**

**Auna fahimta ta biyu (2)**

1. Akwai sunaye na ayoyi da ________ da Hausawa suke amfani da su.
Amsa: - surori

2. Kawo sunayen da Hausawa suke amfani da su na ayoyi guda uku.
Amsa: -
ii. Lantana
iii. Kalafama
iv. Shafa'atu

3. Kawo sunayen surori guda uku da Hausawa suke amfani da su.
Amsa: -
i- Tabara
ii- Ƙuluhiya
iii- Alhaƙatu

4. Cire bare daga cikin waɗannan sunayen Hausawa.
**a-** **Maliku** b- Bara'atu c- Abasa d- Ƙuluhiya

## RUKUNI NA UKU

Kashi na Ɗaya (1) Wasu Sunayen Hausawa
Kashi na Biyu (2) Wasu Sunayen Hausawa
Kashi na uku (3) Wasu Sunayen Hausawa
Kashi na Huɗu (4) Ƙirar Sunayen Hausawa

## Kashi na Ɗaya (1) Wasu Sunayen Hausawa

### Abubuwan da Suke Ciki

1.1 Gabatarwa
1.2 Darasi
1.3 Sunayen Ranaku
 1.3.1 Sunayen Ranaku na Maza
 1.3.2 Sunayen Ranaku na Mata
1.4 Taƙaitawa
1.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
1.6 Manazarta
1.7 Amsoshin Auna Fahimta

## 1.1 Gabatarwa

A cikin wannan kashin, mun gabatar da bayanai kan sunayen da Hausawa suke sanyawa 'ya'yansu, suanyen sun samu ne bayan zuwan musulunci, wato sunaye ne na Mala'iku da ayoyi da kuma surori na Alƙur'ni waɗanda Hausawa suka yi masu 'yar kwaskwarima suke amfani da su a cikin harshen Hausa. Amma a wannan darasin za mu yi bayani ne kan sunayen da Hausawa suke sanya wa 'ya'yansu waɗanda suka shafi sunayen ranaku.

## 1.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan rukuni ɗalibai za su iya:

- Bayani kan sunayen ranaku.
- Zayyana Ire-Iren sunayen ranaku.
- Zayyana wasu sunayen ranaku
- Bambace sunayen ranaku na maza da na mata.

## 1.3 Sunayen Ranaku

Sunayen ranaku na cikin jerin sunayen da Hausawa suke amfani da shi sanyawa 'ya'yansu ta hanyar la'akari da ranar da aka haifi jariri/jaririrya. Ƙarƙashin wannan akwai ɓangarori guda biyu, akwai

ɓangaren sunayen ranaku na maza da na mata. Hausawa suna amfani da ire-iren waɗannan sunaye wajen sanya wa 'ya'yansu.

## 1.3.1 Sunayen Ranaku na Maza

Waɗannan sunaye ne na ranaku waɗanda suka ƙunshi sunayen maza kawai. Ga su kamar haka:

| Sunan Rana | Sunayen Hausawa |
|---|---|
| Asabar | Ɗan Asabe |
| Lahadi | Ɗanladi/Ɗanladidi/Ɗanladiyo/Nalado/Lado |
| Litinin | Ɗanliti/Liti/Ɗantani |
| Talata | Ɗantala/Ɗantata/MaiTala |
| Laraba | Ɗanbala/Ɗanlarai/Bawa/Bala/Balarabe |
| Alhamis | Ɗanlami/Nalami |
| Juma'a | Ɗanjummai/Ɗanjuma/Jume/Najume |

**Auna fahimta ta farko (1)**

1. Akwai sunaye ranaku na _________ da _________ a wajen Hausawa.
2. Kawo sunayen Hausawa na maza na ranar Lahadi guda uku.
3. Ranaku nawa Hausawa suke la'akari da su wajen sanya wa mutum suna?
4. Cire bare daga cikin waɗannan sunayen Hausawa.

 a- Ɗantani b-Ɗantala c-Ɗantata d- Maitala.

## 1.3.1.2 Sunayen Ranaku na Mata

Waɗannan sunaye ne na ranaku waɗanda suka ƙunshi sunayen mata kawai. Ga su kamar haka:

| Sunan Rana | Sunayen Hausawa |
|---|---|
| Asabar | Asibi/Asabe/ Asaberuwa |
| Lahadi | Ladi/Ladidi/Ladiyo/Ladingo |
| Litinin | Atine/Tani/Tine |
| Talata | Talatu/Talatuwa/Tatuwa/Tatu |

| | |
|---|---|
| Laraba | Balaraba/Larai/Laraba/Laro/Tabawa |
| Alhamis | Lami/Lamide/Lamisuwa/Lamimi |
| Juma'a | Jummai/Jummalo/Aljuma |

**Auna fahimta ta biyu (2)**

1- Akwai sunaye ranaku na ________ da ________ a wajen Hausawa.
2- Kawo sunayen Hausawa na mata na ranar Laraba guda uku.
3- Ranaku nawa Hausawa suke la'akari da su wajen sanya wa mutum suna?
4- Cire bare daga cikin waɗannan sunayen Hausawa.
a- Tatuwa b-Talatuwa c- Talatu d- Tabawa.

## 1.5 Taƙaitawa

A wannan kashin, mun yi bayani kan sunayen ranaku waɗanda Hausawa suke amfani da su wajen sanya wa 'ya'yansu. Sannan mun kawo sunayen ranaku na maza da na mata. A ƙarshe, mun nuna kwaskwarimar da suke yi wa wasu sunayen a cikin misalai.

## 1.6 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi

Asabar
Lahadi
Litinin
Laraba
Alhamis
Juma'a

## 1.7 Mnazarta

Abdullahi I.S.S (2008). "Jiya ba Yau Ba: Waiwaye a Kan Al'adun Matakan Rayuwar

Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa." Kundin digiri na uku: Jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto.

Adamu, M. T. (2015). Tasirin Musulunci Kan Sunayen Hausawa. A Cikin *Harsunan Nijeriya*, Vol. XXV: 163-186.

Alhassan da Wasu (1987) *Zaman Hausawa.* Zaria: ABU Press.

Bichi A.Y (2013). *Tsokaci a Kan Bukukuwan Hausawa na Gargajiya wajen cigaban Al'umma*. Zaria: Ahmadu Bello University, Press.

CNHN (1981). *Rayuwar Hausawa*. Lagos: Thomos Nilson Nigeria Limited.

Gusau, G.U (2012). *Bukukuwan Hausawa*. Gusau: Ol-Faith Prints.

**Amsoshin Tambayoyin**

Auna fahimta ta farko (1)

1- Akwai sunaye ranaku na ________ da ________ a wajen Hausawa.
Amsa: - Maza da na mata
2- Kawo sunayen Hausawa na maza na ranar Lahadi guda uku.
Amsa: -
i- Ɗanladi
ii- Ɗanladidi
iii- Ɗanladiyo
iv- Nalado
v- Lado

3- Ranaku nawa Hausawa suke la'akari da su wajen sanya wa mutum suna?
Amsa: - bakwai
4- Cire bare daga cikin waɗannan sunayen Hausawa.
a- **Ɗantani** b-Ɗantala c-Ɗantata d- Maitala.

**Auna fahimta ta biyu (2)**

1- Akwai sunaye ranaku na ________ da ________ a wajen Hausawa.
Amsa: - maz da mata

2- Kawo sunayen Hausawa na mata na ranar Laraba guda uku.
Amsa: -

i- Balaraba
ii- Larai
iii- Laraba
iv- Laro
v- Tabawa
vi-
3- Ranaku nawa Hausawa suke la'akari da su wajen sanya wa mutum suna?

Amsa: - bakwai

4- Cire bare daga cikin waɗannan sunayen Hausawa.
a- Tatuwa b-Talatuwa c- Talatu **d- Tabawa.**

## Kashi na Biyu (2) Wasu Sunayen Hausawa

**Abubuwan da Suke Ciki**

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufar Darasi
2.3 Sunayen na Lokacin Ibada
2.3.1 Sunayen Lokacin Ibada na Maza
2.3.2 Sunayen Lokacin Ibada na Mata
2.4 Taƙaitawa
2.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
2.6 Manazarta
2.7 Amsoshin Auna Fahimta

## 2.1 Gabatarwa

A cikin wannan kashin, mun gabatar da bayanai kan sunayen da Hausawa suke sanyawa 'ya'yansu, sunayen sun samu ne bayan zuwan musulunci, wato sunaye ne na ranaku waɗanda Hausawa sukan yi masu 'yar kwaskwarima suke amfani da su a cikin harshen Hausa. Amma a wannan darasin za mu yi bayani ne kan sunayen da Hausawa suke sanya wa 'ya'yansu waɗanda suka shafi sunaye na lokacin ibada.

## 2.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan rukuni ɗalibai za su iya:

- Bayani kan sunaye na lokacin ibada.
- Zayyana Ire-Iren sunaye na lokacin ibada.
- Zayyana wasu sunaye na lokacin ibada
- Bambace sunaye na lokacin Ibada na maza da na mata.

## 2.3 Sunaye na Lokacin Ibada

Sunaye na lokacin Ibada na cikin jerin sunayen da Hausawa suke amfani da su wajen sanya wa 'ya'yansu ta hanyar la'akari da lokacin da aka haifi jariri/jaririrya, kamar lokacin yin salla ko lokacin azumi ko daren salla babba ko ƙarama da sauransu. Ƙarƙashin wannan akwai ɓangarori guda biyu, akwai ɓangaren sunaye na lokacin ibada na maza da na mata. Hausawa suna amfani da ire-iren waɗannan sunaye wajen sanya wa 'ya'yansu.

### 2.3.1 Sunaye na lokacin ibada na Maza

Waɗannan sunaye ne na lokacin ibada waɗanda suka ƙunshi sunayen maza kawai. Ga su kamar haka:

| Lokuta | Sunayen Hausawa |
|---|---|
| Daren ƙaramar salla | Sallah/Masallaci/ Nasalla |
| Daren babbar salla | Alhaji/Alhajiji/Hajjin/Kaila |
| Watan Azumi | Ɗan'Azumi/Labaran/Lamarana |
| Takutala | Na'Annabi/ Na Manzo |
| Hanyar tafi ko dawo daga Makka | Yawale |

**Auna fahimta ta farko (1)**

1- Akwai sunaye na lokacin ibada na ________ da ________ a wajen Hausawa.
2- Kawo sunayen Hausawa na maza na ranar daren babbar salla guda uku.
3- Lokutan ibada nawa Hausawa suke la'akari da su wajen sanya wa mutum suna?
4- Cire bare daga cikin waɗannan sunayen Hausawa.
a- babbar salla b- Azumi c- Takutaha d- haihuwa.

### 2.3.2 Sunaye na lokacin ibada na Maza

Waɗannan sunaye ne na lokacin ibada waɗanda suka ƙunshi sunayen mata kawai. Ga su kamar haka:

| Lokuta | Sunayen Hausawa |
|---|---|
| Daren ƙaramar salla | Tasalla/Tasalluwa |
| Daren babbar salla | Hajiya/Hajiyayye/Hajjaju/Hajjo/Baitu |
| Watan Azumi | Azimi/Lamara |
| Takutala | Ta'Annabi/Ta Rasulu |
| Hanyar tafi ko dawo daga Makka | Yabi |

**Auna fahimta ta biyu (2)**

1. Akwai sunaye na lokacin ibada na ________ da ________ a wajen Hausawa.
2. Kawo sunayen Hausawa na mata na watan azumi guda uku.
3. Lokutan ibada nawa Hausawa suke la'akari da su wajen sanya wa mutum suna?
4. Cire bare daga cikin waɗannan sunayen Hausawa.
   a- babbar salla b- Azumi c- Takutaha d- haihuwa.

## 2.4 Taƙaitawa

A wannan kashin, mun yi bayani kan sunaye na lokutan ibada waɗanda Hausawa suke amfani da su wajen sanya wa 'ya'yansu. Sannan mun kawo sunaye na lokacin ibada na maza da na mata. A ƙarshe, mun nuna kwaskwarimar da suke yi wa wasu sunayen a cikin misalai.

## 2.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi

Babbar salla-
Ƙaramar salla-
Watan Azumi-
Takutaha-

## 2.6 Manazarta

Abdullahi I.S.S (2008). "Jiya ba Yau Ba: Waiwaye a Kan Al'adun Matakan Rayuwar

Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa." Kundin digiri na uku: Jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto.

Adamu, M. T. (2015). Tasirin Musulunci Kan Sunayen Hausawa. A Cikin *Harsunan Nijeriya*, Vol. XXV: 163-186.

Alhassan da Wasu (1987) *Zaman Hausawa*. Zaria: ABU Press.

Bichi A.Y (2013). *Tsokaci a Kan Bukukuwan Hausawa na Gargajiya wajen cigaban Al'umma*. Zaria: Ahmadu Bello University, Press.

CNHN (1981). *Rayuwar Hausawa*. Lagos: Thomos Nilson Nigeria Limited.

Gusau, G.U (2012). *Bukukuwan Hausawa*. Gusau: Ol-Faith Prints.

**Amsoshin Tambayoyin**

**Auna fahimta ta farko (1)**

1- Akwai sunaye na lokacin ibada na ________ da ________ a wajen Hausawa.
Amsa: - maza da na mata

2- Kawo sunayen Hausawa na maza na ranar daren babbar salla guda uku.
Amsa: -
i- Alhaji
ii- Alhajiji
iii- Hajjin
iv- Kaila

3- Lokutan ibada nawa Hausawa suke la'akari da su wajen sanya wa mutum suna?
Amsa: - biyar

4- Cire bare daga cikin wadannan sunayen Hausawa.
a- babbar salla b- Azumi c- Takutaha **d- haihuwa**.

**Auna fahimta ta biyu (2)**

1. Akwai sunaye na lokacin ibada na ________ da ________ a wajen Hausawa.
Amsa: - maza da na mata
2. Kawo sunayen Hausawa na mata na watan azumi guda biyu.
Amsa: -
i- Azimi
ii- Lamara
3. Lokutan ibada nawa Hausawa suke la'akari da su wajen sanya wa mutum suna?
Amsa: - biyar
4. Cire bare daga cikin wadannan sunayen Hausawa.
a- babbar salla b- Azumi c- Takutaha **d- haihuwa.**

## Kashi na uku (3) Wasu Sunayen Hausawa

### Abubuwan da Suke Ciki

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufar Darasi
3.3 Sunayen na Sha'awa
 3.3.1 Sunayen Sha'awa na Maza
 3.3.2 Sunayen Sha'awa na Mata
3.4 Taƙaitawa
3.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
3.6 Manazarta
3.7 Amsoshin Auna Fahimta

## 2.1 Gabatarwa

A cikin wannan kashin, mun gabatar da bayanai kan sunayen da Hausawa suke sanyawa 'ya'yansu, sunayen sun samu ne bayan zuwan musulunci, wato sunaye ne na lokutan ibada waɗanda Hausawa sukan yi masu 'yar kwaskwarima suke amfani da su a cikin harshen Hausa. Amma a wannan darasin za mu yi bayani ne kan sunayen da Hausawa suke sanya wa 'ya'yansu waɗanda suka shafi sunaye na sha'awa.

## 3.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan rukuni ɗalibai za su iya:

- Bayani kan sunaye na sha'awa.
- Zayyana Ire-Iren sunaye na sha'awa.
- Zayyana wasu sunaye na sha'awa
- Bambace sunaye sha'awa na maza da na mata.

## 3.3 Sunayen Sha'awa

Sunayen sha'awa na cikin jerin sunayen da Hausawa suke amfani da su wajen sanya wa 'ya'yansu ta hanyar yin aron wasu kalmomi daga harshen Larabci suna amfani da su a matsayin sunaye. Kalmomin sun shafi wasu abubuwa kamar sunayen dabbobi da tsirrrai da duwatsu da wurare kuma sunaye waɗanda ba su da wata ma'ana sam-sam. Ƙarƙashin wannan akwai ɓangarori guda biyu, akwai ɓangaren sunaye na sha'awa na maza da na mata. Hausawa suna amfani da ire-iren waɗannan sunaye wajen kiran 'ya'yansu da su.

### 3.3.1 Sunayen Sha'awa na Maza

Akwai sunaye na sha'awa kuma al'ummar Hausawa suna ɗaya daga cikin rukunin mutanen da suke amfani da irin waɗannan sunaye wajen sanya wa 'ya'yansu bisa wata sha'awa a lokacin da aka haifi jaririn ko jaririyar. Ga sunayen sha'awa na maza kamar haka:

| Sunaye | Ma'anarsu |
|---|---|
| Zamil | Abokin zama |
| Tajo | Kambun mulki |
| Fa'iz | Mai nasara |
| Kamal | Cika |
| Faisal | Madatsi |
| Jamal | Kyau |
| Rajab | Sunan wata |
| Mahir | Kwararre |
| Fa'iz | Mai nasara |
| Amir | sarki |

**Auna fahimta ta farko (1)**

1- Akwai sunayen sha'awa _________ da _________ a wajen Hausawa.
2- Kawo sunayen uku na abubuwan da Hausawa suke laƙari da su wajen sanya sunan sha'awa.
3- Kawo ma'anar waɗannan sunayen.
   i- Kamal
   ii- Jamal
   iii- Tajo
   iv- Fa'iz
   v- Cire bare daga cikin waɗannan sunayen Hausawa.
a- Fa'iz b- Faisal c- Salwa d- Mahir.

### 3.3.2 Sunayen Sha'awa na Mata

Akwai sunaye na sha'awa kuma al'ummar Hausawa suna ɗaya daga cikin rukunin mutanen da suke amfani da irin waɗannan sunaye wajen

sanya wa ‘ya’yansu bisa wata sha’awa a lokacin da aka haifi jaririn ko jaririyar. Ga sunayen sha’awa na mata kamar haka:

| Sunaye | Ma’anarsu |
|---|---|
| Ahlan | Mafarki |
| Aliya | Maigirma |
| Bahijja | Murna |
| Basama | Mai fara’a |
| Fatahiyya | Mabuɗi |
| Sarwa | Dukiya |
| Sakina | Natsuwa |
| Rashida | Kintsattsiya |
| Laɗifa | Tatausa |
| Fir’dausi | Sunan Aljanna |
| Salwa | tsuntsuwa |

**Auna fahimta ta biyu (2)**

1- Akwai sunayen sha’awa ________ da ________ a wajen Hausawa.
2- Kawo sunayen uku na abubuwan da Hausawa suke laƙari da su wajen sanya sunan sha’awa.
3- Kawo ma’anar waɗannan sunayen.
   i- Fiddausi
   ii- Bahijja
   iii- Basama
   iv- Laɗifa
4- Cire bare daga cikin waɗannan sunayen Hausawa.
a- Fa’iz b- Basama c- Sarwa d- Rashida.

## 3.5 Taƙaitawa

A wannan kashin, mun yi bayani kan sunaye na sha’awa waɗanda Hausawa suke amfani da su wajen sanya wa ‘ya’yansu. Sannan mun kawo sunaye na sha’awa na maza da na mata. A ƙarshe, mun nuna kwaskwarimar da suke yi wa wasu sunayen a cikin misalai.

## 3.6 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi

Rajab – sunan wata
Firdausi - sunan Aljanna ne
Salwa - sunan tsutsuwa
Tajo – kambun mulki
Jamal – abun mai kyau

## 3.7 Manazarta

Abdullahi I.S.S (2008). "Jiya ba Yau Ba: Waiwaye a Kan Al'adun Matakan Rayuwar

Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa." Kundin digiri na uku: Jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto.

Adamu, M. T. (2015). Tasirin Musulunci Kan Sunayen Hausawa. A Cikin *Harsunan Nijeriya,* Vol. XXV: 163-186.

Alhassan da Wasu (1987) *Zaman Hausawa.* Zaria: ABU Press.

Bichi A.Y (2013). *Tsokaci a Kan Bukukuwan Hausawa na Gargajiya wajen cigaban Al'umma*. Zaria: Ahmadu Bello University, Press.

CNHN (1981). *Rayuwar Hausawa*. Lagos: Thomos Nilson Nigeria Limited.

Gusau, G.U (2012). *Bukukuwan Hausawa*. Gusau: Ol-Faith Prints.

**Amsoshin Tambayoyin**

**Auna fahimta ta farko (1)**

1- Akwai sunayen sha'awa ________ da ________ a wajen Hausawa.
Amsa: -maza da na mata

2- Kawo sunayen uku na abubuwan da Hausawa suke laƙari da su wajen sanya sunan sha'awa.

3- Kawo ma'anar waɗannan sunayen.

i- Kamal
ii- Jamal
iii- Tajo
iv- Fa'iz

4- Cire bare daga cikin waɗannan sunayen Hausawa.
a- Fa'iz b- Faisal c- Salwa d- Mahir.

1- Auna fahimta ta biyu (2) Akwai sunayen sha'awa ________ da ________ a wajen Hausawa.
Amsa: maza da mata

2- Kawo sunayen uku na abubuwan da Hausawa suke laƙari da su wajen sanya sunan sha'awa.
Amsa: -
i- Dabbobi
ii- Tsirrai
iii- Duwatsu da sauransu

3- Kawo ma'anar waɗannan sunayen.
i- Fiddausi
ii- Bahijja
iii- Basama
iv- Laɗifa

Amsa: -

i- sunan aljanna
ii- murna
iii- mai fara'a
iv- mai laushi

4- Cire bare daga cikin waɗannan sunayen Hausawa.
a- **Fa'iz** b- Basama c- Sarwa d- Rashida.

## Kashi na Huɗu (4) Ƙirar Sunayen Hausawa

**Abubuwan da Suke Ciki**

4.1 Gabatarwa
4.2 Manufar Darasi
4.3 Ma'anar Ƙirar da Hanyoyin Ƙirar Kalma (sunaye)
4.3.1 Hanyar Ƙirar Saƙandami (Acronyms) ta Sunayen Hausawa Maza
4.3.2 Hanyar Ƙirar Saƙandami (Acronyms) ta Sunayen Hausawa Mata
4.4 Taƙaitawa
4.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
4.6 Manazarta
4.7 Amsoshin Auna Fahimta

### 4.1 Gabatarwa

A cikin kashin da ya gabata, mun gabatar da bayanai kan sunayen da Hausawa suke sanyawa 'ya'yansu, waɗanda sun samu ne bayan zuwan Musulunci, wato sunaye ne na sha'awa waɗanda Hausawa sukan yi masu 'yar kwaskwarima su yi amfani da su a cikin harshen Hausa. Amma a wannan darasin za mu yi bayani ne kan yadda ake samar da sunayen Hausawa ta hanyar ƙirar Saƙandami (Acronyms).

### 4.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan rukuni ɗalibai za su iya:

- Bayani kan ƙirar kalma.
- Zayyana Ire-Iren Hanyoyin ƙirar Kalma.
- Zayyana sunayen Hausawa ta hanyar ƙirar Saƙandami
- Bambace sunayen maza da na mata ta fuskar Saƙandami.

### 4.3 Ƙirar

Ƙirar kalma reshe ne na nahawu wanda yake nazarin sigogin fasalin kalmomi ta la'akari da tubalin ginin kalma ƙwayar kalma" (Amfani, 2007:139). Kuma za mu iya cewa ƙirar kalma wata hanya ce da ake bi domin samar da samar da sabuwar kalma ko canza wa kalma siffa, kamar Taƙaitawa ko Takurewa ko Saƙandami da sauransu. Akwai hanyoyi da ake amfani da su wajen ƙirar kalma ta sunayen Hausawa. Hanyoyin su ne:

i- Saƙandami
ii- Ragau

iii- Markaɗau
iv- Takurau
v- Gutsirau

## Saƙandami

Saƙadami wata hanya ce da masu ilimin ƙirar kalma/kalmomi suke amfani da ita wajen taƙaita kalma, ta hanyar zaɓin wasu baƙaƙe farko na kowacce kalma a haɗa kuma su yi wakilci, a wani lokaci sun kan samar da sabuwar kalma (Gwammaja, ). Irin wannan dabara ta saƙandami an fi samu ta a cikin harshen Ingilishi, amma ana samu a sauran harsuna, ga wasu misalai, *T.V* (tele - vision) da *U.N* (United Nations) *W.H.O* (world health organization) da sauransu.

### 4.3.1 Hanyar Ƙirar Saƙandami (Acronyms) ta Sunayen Hausawa Maza

Akwai sunayen Hausawa maza da ake yi wa Saƙandami a tsarin ƙirar kalma. Ana yin Saƙandami ne ta hanyar zaɓar wasu baƙaƙe guda biya, ma'ana a farkon gaɓa ko ta biyu wani zubin har zuwa ta uku. Ga su kamar haka:

| Cikakken Suna | Saƙandami |
|---|---|
| Tijjani | TJ |
| Jibrin | JB |
| Kabir | KB |
| Tukur | TK |
| Dikko | DK |
| Abdulkarim | AK |
| Kamal | KM |

**Auna fahimta ta farko (1)**

1- Shin akwai ƙirar Sakandami a sunayen Hausawa?
2- Kawo sunayen Hausawa uku da ake yi masu Saƙandami na maza.
3- Kawo cikakken waɗannan sunaye.
i- KL
ii- TK
iii- KB
iv- TJ
4- Wane ne Saƙandamin Tukur?

## 4.3.2 Hanyar Ƙirar Saƙandami (Acronyms) ta Sunayen Hausawa Mata

Akwai sunayen Hausawa mata da ake yi wa Saƙandami a tsarin ƙirar kalma. Ana yin Saƙandami ne ta hanyar zaɓar wasu baƙaƙe guda biya, ma’ana a farkon gaɓa ko ta biyu wani zubin har zuwa ta uku. Ga su kamar haka:

| Cikakken Suna | Saƙandami |
|---|---|
| Bilkisu | BK |
| Rabi | RB |
| Salma | SM |
| Lami | LM |
| Mariya | MR |
| Hadiza | HD |
| Habiba | HB |

**Auna fahimta ta biyu (2)**

1. Shin akwai ƙirar Sakandami a sunayen Hausawa?
2. Kawo sunayen Hausawa uku da ake yi masu Saƙandami na mata.
3. Kawo cikakken waɗannan sunaye.

i- HD
ii- HB
iii- LM
iv- SM

4- Wane ne Saƙandamin Habiba?

## 4.4 Taƙaitawa

A wannan kashin, mun kawo bayani kan sunayen Hausawa waɗanda ake yi amfani da hanyar ƙira ta Sakandami. Irin waɗannan sunaye matasa ne suka fi yin amfani da su wajen kiran abokai ko ƙawaye. Sannan mun kawo sunayen Hausawa na maza da na mata. A ƙarshe, mun nuna irin kwaskwarimar da matasa suke yi wa wasu sunayen Hausawa a cikin misalai.

## 4.5 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi

Saƙandami –
Ƙira –
Kalma -

## 4.6 Manazarta

Abdullahi I.S.S (2008). "Jiya ba Yau Ba: Waiwaye a Kan Al'adun Matakan Rayuwar

Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa." Kundin digiri na uku: Jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto.

Adamu, M. T. (2015). Tasirin Musulunci Kan Sunayen Hausawa. A Cikin *Harsunan Nijeriya,* Vol. XXV: 163-186.

Alhassan da Wasu (1987) *Zaman Hausawa.* Zaria: ABU Press.

Amfani, A.H. (2007). Hausa Morphology. In *Basic Linguistics for Nigerian Languages Teachers.* (ed) Ore Yusuf. Port Harcourt: M&J Grand Orbit Communication Ltd.

Bichi A.Y (2013). *Tsokaci a Kan Bukukuwan Hausawa na Gargajiya wajen cigaban Al'umma*. Zaria: Ahmadu Bello University, Press.

CNHN (1981). *Rayuwar Hausawa*. Lagos: Thomos Nilson Nigeria Limited.

Gwammaja, I. G. (nd). Tsokaci Kan Tasarifi a Cikin Waƙoƙin Dakta Mamman Shata.

Gusau, G.U (2012). *Bukukuwan Hausawa*. Gusau: Ol-Faith Prints.

Plag, I. (2002). *Word-Formation in English*. Siegea: Cambridge University Press.

Sani, Ɗ. (2002) Word- Formation in Hausa (A case study of derivation Functional shift and clipping) Ph. D dissertation. Bayero University, Kano.

**Amsoshin Tambayoyin**

Auna fahimta ta farko (1)

1- Shin akwai ƙirar Sakandami a sunayen Hausawa?
Amsa: - Haka ne
2- Kawo sunayen Hausawa uku da ake yi masu Saƙandami na maza.
Amsa: -
i- Kabiru
ii- Tijjani
iii- Tukur
iv- Jabirin da sauransu
3- Kawo cikakken waɗannan sunaye.
i- KL
ii- TK
iii- KB
iv- TJ

Amsa: -

i- Kamal
ii- Tukur
iii- Kabir
iv- Tijjani

4- Wane ne Saƙandamin Tukur?
Amsa: - TK

**Auna fahimta ta biyu (2)**

1. Shin akwai ƙirar Sakandami a sunayen Hausawa?
Amsa: - Ee
2. Kawo sunayen Hausawa uku da ake yi masu Saƙandami na mata.
Amsa: -
i- Habiba
ii- Lami
iii- Hadiza
iv- Bilki
v- Rabi da sauransu
3. Kawo cikakken waɗannan sunaye.
i- HD
ii- HB
iii- LM
iv- SM

Amsa: -

i- Hadiza
ii- Habiba
iii- Lami
iv- Salma

4- Wane ne Saƙandamin suanan Habiba?
Amsa: - HB

**RUKUNI NA HUƊU (4)**


| | |
|---|---|
| Kashi na Ɗaya (1) | Ƙirar Sunayen Hausawa |
| Kashi na Biyu (2) | Ƙirar Sunayen Hausawa |
| Kashi na uku (3) | Sunayen Hausawa na Dangantaka |


## Kashi na Ɗaya (1) Ƙirar Sunayen Hausawa

**Abubuwan da Suke Ciki**


1.1 Gabatarwa
1.2 Manufar Darasi
1.3 Ragau (Clipping)
1.3.1 Hanyar Ƙirar Ragau (Clipping) ta Sunayen Hausawa Maza
1.3.2 Hanyar Ƙirar Ragau (Clipping) ta Sunayen Hausawa Mata
1.4 Taƙaitawa
1.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
1.6 Manazarta
1.7 Amsoshin Auna Fahimta


## 1.1 Gabatarwa

A cikin kashin da ya gabata, mun gabatar da bayanai kan sunayen da Hausawa suke sanyawa 'ya'yansu, waɗanda sun samu ne a sanadiyyar wayewa da ilimin boko, wato sunaye ne na ƙirƙira da matasa (maza da mata) suke yi wa 'yar kwaskwarima su yi amfani da su a cikin harshen Hausa. Amma a wannan darasin za mu yi bayani ne kan yadda ake ƙirar Ragau domin samar da sunayen Hausawa da matasa suke amfani da su a yau.

## 1.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan rukuni ɗalibai za su iya:

- Bayani kan ƙirar Ragau.
- Zayyana Ire-Iren Ragau.
- Zayyana sunayen Hausawa ta hanyar ƙirar Ragau.
- Bambace sunayen maza da na mata ta fuskar ƙirar Ragau.

## 1.3 Ragau (Clipping)

Kamar yadda masana dama suka bayyana cewa "wannan hikima na ɗaya daga cikin sinadarai da ake amfani da su wajen ƙirar sabuwar kalma a ɓangaren tasarifi kuma ana gudanar da irin wannan dabara ta hanyar rage wani ɓangare na farko ko tsakiya ko kuma ƙarshen kalma domin a

samar da sabuwar kalma" (Plag: 146). Za mu iya cewa, Ragau hanya ce ta rage wani sashe na kalma domin a samar da sabuwar kalma. Akan samu Ragau a farko ko tsakiya kon ƙarshen kalmar suna. Kamar Hajara – Jaru/Haja da A'isha – A'I/Shatu da sauransu.

### 1.3.1 Hanyar Ƙirar Ragau (Clipping) ta Sunayen Hausawa Maza

Akwai sunayen Hausawa maza da ake yi wa Ragau a tsarin ƙirar kalma. Ana yin Ragau ne ta hanyar raje wasu baƙaƙe ko gaɓar farko ta ƙarshen kalma. Ana yi wa sunayen Musulunci da na zamani Ragau. Ga su kamar haka:

| Cikakken Suna | Ragau |
|---|---|
| Adamu | Ada/Ado |
| Sulaiman | Sule |
| Sama'ila | Ila |
| Ibrahim | Iro |
| Haruna | Haru |
| Muhammadu | Madu/Mado |
| Hamisu | Hami |
| Tasi'u | Tasi |
| Sadisu | Sadi |
| Mika'il | Mika/Ka'ilu/Miko/Kaila |
| Alƙasim | Ƙasim/Alƙa |

Sai kuma ɗaya hanyar wadda 'yanmata da samari suke ƙirƙira sunayen da Hausawa suke amfani da su waɗanda ake samarwa ta hanyar ragau, ga su kamar haka:

| Cikakken Suna | Ragau |
|---|---|
| Nasuru | Nas |
| Bashir | Bas |
| Nura | Nur |
| Sani | San |
| Yasir | Yas |
| Shamsu | Shamo |
| Usman | Usi |
| Adamu | Adam |
| Ibrahim | Ibro |

## Auna fahimta ta farko (1)

1- Shin akwai ƙirar Ragau a sunayen Hausawa na maza?
2- Kawo sunayen Hausawa uku da ake yi masu Ragau na maza.
3- Kawo cikakken sunayen waɗannan.
    i- Shamo

| |
|---|
| ii- Hami<br>iii- Tasi<br>iv- Usi<br>4- Ya ya sunan Haruna zai kasance idan an ragau? |

## 1.3.2 Hanyar Ƙirar Ragau (Clipping) ta Sunayen Hausawa Mata

Akwai sunayen Hausawa mata da ake yi wa Ragau a tsarin ƙirar kalma. Ana yin ragau ne ta hanyar zaɓar wasu baƙaƙe ko gaɓar a farko ko ƙarshen kalma. Ana yi wa sunayen Musulunci da na zamani Ragau, kamar haka:

| Cikakken Suna | Ragau |
|---|---|
| Amina | Mina |
| Hadiza | Dije |
| Safiya | Safi |
| Mariya | Mari |
| A'isha | A'i |
| Fatima | Fati |
| Hajara | Hajjo |
| Zulaiha | Zilai |
| Rabiya | Rabi |
| Salamatu | Salma |
| Nafisa | Nafi |
| Lubabatu | Lube/Luba |
| Sa'adatu | Sa'a |

Sai kuma ɗaya hanyar wadda 'yanmata da samari suke ƙirƙira sunayen da Hausawa suke amfani da su waɗanda ake samarwa ta hanyar ragau, ga su kamar haka:

| Cikakken Suna | Ragau |
|---|---|
| Fiddausi | Fido |
| Ruƙayya | Ruky |
| Badiya | Bady |
| Asma'u | Asma/Amsy |
| Nusaiba | Nusy |
| Ramatu | Ramsy |
| Nafisa | Nafsy |
| Jamila | Jamsy |
| Habiba | Habsy |

**Auna fahimta ta biyu (2)**

| |
|---|
| 1- Shin akwai ƙirar Ragau a sunayen Hausawa na mata?<br>2- Kawo sunayen Hausawa guda uku da ake yi masu Ragau na mata.<br>3- Kawo cikakken sunayen waɗannan. |

i- Fiddo
ii- Rabi
iii- Nafi
iv- Ruƙa/Ruƙy
4- Ya ya sunan Mariya zai kasance idan an ragau?

## 1.4 Taƙaitawa (Summary)

A wannan kashin, mun kawo bayani kan sunayen Hausawa waɗanda ake samarwa ta hanyar amfani ƙira ta Ragau. Irin waɗannan sunayen matasa ne ƙirƙira su tare da yin amfani da su wajen kiran abokai ko ƙawaye. Sannan mun kawo misalai na sunayen Hausawa na maza da na mata. A ƙarshe, mun nuna irin kwaskwarimar da matasa suke yi wa wasu sunaye na Hausawa.

## 1.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi

Ragau –
Shamo –
Hami -

## 1.6 Manazarta

Abdullahi I.S.S (2008). "Jiya ba Yau Ba: Waiwaye a Kan Al'adun Matakan Rayuwar

Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa." Kundin digiri na uku: Jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto.

Adamu, M. T. (2015). Tasirin Musulunci Kan Sunayen Hausawa. A Cikin *Harsunan Nijeriya*, Vol. XXV: 163-186.

Alhassan da Wasu (1987) *Zaman Hausawa.* Zaria: ABU Press.

Amfani, A.H. (2007). Hausa Morphology. In *Basic Linguistics for Nigerian Languages Teachers.* (ed) Ore Yusuf. Port Harcourt: M&J Grand Orbit Communication Ltd.

Bichi A.Y (2013). *Tsokaci a Kan Bukukuwan Hausawa na Gargajiya wajen cigaban Al'umma*. Zaria: Ahmadu Bello University, Press.

CNHN (1981). *Rayuwar Hausawa*. Lagos: Thomos Nilson Nigeria Limited.

Gwammaja, I. G. (nd). Tsokaci Kan Tasarifi a Cikin Waƙoƙin Dakta Mamman Shata.

Gusau, G.U (2012). *Bukukuwan Hausawa*. Gusau: Ol-Faith Prints.

Plag, I. (2002). *Word-Formation in English*. Siegea: Cambridge University Press.

Sani, Ɗ. (2002) Word- Formation in Hausa (A case study of derivation Functional shift and clipping) Ph. D dissertation. Bayero University, Kano.

## 1.7 Amsoshin Tambayoyin

Auna fahimta ta farko (1)

1- Shin akwai ƙirar Ragau a sunayen Hausawa na maza?
Amsa: -Ee
2- Kawo sunayen Hausawa guda uku da ake yi masu Ragau na maza.
Amsa: -
i- Habibu
ii- Hamisu
iii- Nasuru
iv- Tasi'u
v- Sadiƙu da sauransu.
3- Kawo cikakken sunayen waɗannan.
i- Shamo
ii- Hami
iii- Tasi
iv- Usi

Amsa: -

i- Shamsu
ii- Hamisu
iii- Tasi'u
iv- Usman

4- Ya ya sunan Haruna zai kasance idan an ƙirar ragau?

Amsa: - Haru

**Auna fahimta ta biyu (2)**

1- Shin akwai ƙirar Ragau a sunayen Hausawa na mata?
Amsa:- Ee
2- Kawo sunayen Hausawa guda uku da ake yi masu Ragau na mata.
Amsa: -

i- Amina
ii- Habiba
iii- Salamatu
iv- Hindatu da sauransu

3- Kawo cikakken sunayen waɗannan.
   i- Fiddo
   ii- Rabi
   iii- Nafi
   iv- Ruƙa/Ruƙy

Amsa: -

i- Fiddausi
ii- Rabiya
iii- Nafisa
iv- Ruƙayya

4- Ya ya sunan Mariya zai kasance idan an yi ƙirar ragau?
   Amsa ; - Mari

# Kashi na Biyu (2) Ƙirar Sunayen Hausawa

**Abubuwan da Suke Ciki**

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufar Darasi
2.3 Markaɗau (Blending)
  2.3.1 Hanyar Ƙirar Markaɗau (Blending)
  2.3.2 Hanyar Ƙirar Sunayen Hausawa ta Ɗafa-ƙeya
2.4 Taƙaitawa
2.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
2.6 Manazarta
2.7 Amsoshin Auna Fahimta

## 2.1 Gabatarwa

A cikin kashin da ya gabata, mun gabatar da bayanai kan sunayen da Hausawa da suke sanyawa 'ya'yansu, waɗanda aka samar da su a sanadiyyar wayewa da ilimin boko, wato sunaye ne na ƙirƙira da matasa (maza da mata) wato, Ragau da suke yi wa 'yar kwaskwarima su yi amfani da su a cikin harshen Hausa. Amma a wannan darasin za mu yi bayani ne kan yadda ake ƙirar Markaɗau (Blending) domin samar da sunayen Hausawa da matasa suke amfani da su a yau.

## 2.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan rukuni ɗalibai za su iya:

- Bayani kan ƙirar Markaɗau.
- Zayyana sunayen Markaɗau.
- Kawo ma'anar sunayen masu ɗafa-ƙeya.
- Kawo sunayen mata da ake yi wa ɗafa-ƙeya.

## 2.3 Markaɗau (Blending)

Makaɗau wata hikima ce da ake amfani da ita wajen ƙirar sunayen Hausawa. Makaɗau na ƙunsar ɓangaren wata kalma da wata ko kuma a haɗe kalmomi guda biyu su koma guda ɗaya. Matasa su ne suka fi amfani da wannan hikima, ta hanyar kawo sunan farko na Hausa su haɗa da wata kalmar aro daga harshen Ingilishi watau son, inda za ka ji idan sun furta suna sai sautin ya yi kamar na kalmar Ingilishi amma dai Hausawa suke amfani da sunayen a matsayin nasu (Yahaya, 2012: 143-144).

### 2.3.1 Hanyar Ƙirar Markaɗau (Blending) ta Sunayen Hausawa Maza

Akwai sunayen Hausawa maza da ake yi wa Markaɗau a matsayin wata hanya ta ƙirar sabon suna ko kalma. Ana yin Markaɗau ne ta hanyar amfani da ɓangare na wata kalma da wata ko na dukkan kalmomi. Ana amfani da sunan Hausawa a kalmar farko sannan a kawo kalmar Ingilishi a haɗa sai a sami sabon suna a Hausa kamar haka:

| Cikakken Sunaye | Markaɗau |
|---|---|
| Labaran + son | Labson |
| Rabi'u + son | Rabson |
| Jibrin + son | Jibson |
| Ibrahim + son | Ibson |
| Yakubu + son | Harson |
| Haruna + son | Harson |
| Hamisu + son | Hamson |
| Tasi'u + son | Tason |
| Baba + son | babson |
| Miko + son | Mikson |

**Auna fahimta ta farko (1)**

1- Me ake nufi da ƙira Markaɗau?
2- Kawo sunayen Hausawa uku da ake yi masu ƙirar markaɗau.
3- Kawo cikakken sunayen Hausawa.
   i- Labson
   ii- Yakson
   iii- Jibson
   iv- Babson
4- Ya ya sunan Kabiru zai kasance idan an yi markaɗau?

### 2.3.2 Hanyar Ƙirar Sunayen Hausawa ta Ɗafa-ƙeya

Wannan ma, wata hanya ce da ake samar da sababbin sunaye na Hausawa wadda ake amfani da hanyar ɗafa-ƙeya ma'ana, a ƙara wani ɗafi a ƙashen sunan Hausawa domin samar da sabon suna. Wannan hanya samari ne suka fi amfani da ita (Yahaya, 2012: 143-144). Ga misalai:

| Suna + ncy | Saƙandami |
|---|---|
| Amina + ncy | Amina**ncy** |
| Umma + ncy | Umma**ncy** |
| Safiya + ncy | Safiya**ncy** |
| Jamila + ncy | Jamila**ncy** |

| | |
|---|---|
| Salma + ncy | Salma**ncy** |
| Fatima + ncy | Fatima**ncy** |
| Hajara + ncy | Hajara**ncy** |
| Nana + ncy | Nana**ncy** |
| Rabiya + ncy | Rabiya**ncy** |
| Zaliha + ncy | Zaliha**ncy** |

**Auna fahimta ta biyu (2)**

1- Me ake nufi da Ɗafa-ƙeya?
2- Kawo sunayen Hausawa uku da ake yi masu ƙirar Ɗafa-ƙeya.
3- Kawo cikakken sunayen Hausawa.
   i- Ummancy
   ii- Aminancy
   iii- Nafisancy
   iv- Salmancy
4- Ya ya sunan Rabiya zai kasance idan an yi ɗafa-ƙeya?

## 2.4 Taƙaitawa

A wannan kashin, mun kawo bayani kan sunayen Hausawa waɗanda ake samarwa ta hanyar amfani ƙira ta markaɗau da ɗafa-goshi. Irin waɗannan sunayen da ake samarwa ta waɗannan hanyoyi matasa ne suke ƙirƙirarsu tare da yin amfani da su wajen kiran abokai ko ƙawaye. Sannan mun kawo misalai na sunayen Hausawa ta hanyar markaɗau da ɗafa-goshi. A ƙarshe, mun nuna irin kwaskwarimar da matasa suke yi wa wasu sunayen Hausawa.

## 2.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi

Markaɗau – haɗe kalmomi guda biyu waje ɗaya
Ɗafa-ƙeya– ƙarin da ake yi kalma a ƙarshen kalma
Son - suna ne ake kiran yaro namiji a harshen Ingilishi

## 2.6 Manazarta

Abdullahi I.S.S (2008). "Jiya ba Yau Ba: Waiwaye a Kan Al'adun Matakan Rayuwar

Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa." Kundin digiri na uku: Jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto.

Adamu, M. T. (2015). Tasirin Musulunci Kan Sunayen Hausawa. A Cikin *Harsunan Nijeriya*, Vol. XXV: 163-186.

Alhassan da Wasu (1987) *Zaman Hausawa.* Zaria: ABU Press.

Amfani, A.H. (2007). Hausa Morphology. In *Basic Linguistics for Nigerian Languages*

*Teachers.* (ed) Ore Yusuf. Port Harcourt: M&J Grand Orbit Communication Ltd.

Bichi A.Y (2013). *Tsokaci a Kan Bukukuwan Hausawa na Gargajiya wajen cigaban*

*Al'umma*. Zaria: Ahmadu Bello University, Press.

CNHN (1981). *Rayuwar Hausawa*. Lagos: Thomos Nilson Nigeria Limited.

Gwammaja, I. G. (nd). Tsokaci Kan Tasarifi a Cikin Waƙoƙin Dakta Mamman Shata.

Gusau, G.U (2012). *Bukukuwan Hausawa*. Gusau: Ol-Faith Prints.

Plag, I. (2002). *Word-Formation in English*. Siegea: Cambridge University Press.

Sani, Ɗ. (2002) Word- Formation in Hausa (A case study of derivation Functional shift and clipping) Ph. D dissertation. Bayero University, Kano.

Yahaya, N. (2012). Personal Name as a Source of Nickname Formation Among Huasa

Youth. KAjoLLS Katsina Journal of Linguistic & Literary Studies. Vol. 1, No1, pp. 139- 145.

## 2.7 Amsoshin Tambayoyin

Auna fahimta ta farko (1)

1- Me ake nufi da ƙira Markaɗau?

Amsa: -

Makaɗau wata hikima ce da ake amfani da ita wajen ƙirar sunayen Hausawa. Makaɗau na ƙunsar ɓangaren wata kalma da wata ko kuma a haɗe kalmomi guda biyu su koma guda ɗaya

2- Kawo sunayen Hausawa uku da ake yi masu ƙirar markaɗau.
Amsa: -
i- Yakubu
ii- Ibrahim
iii- Jibrin
iv- Labaran
v- Baba da sauransu

3- Kawo cikakken sunayen Hausawa.
i- Labson
ii- Yakson
iii- Jibson
iv- Babson
Amsa: -
i- Labaran
ii- Yakubu
iii- Jibrin
iv- Baba

4- Ya ya sunan jibrin zai kasance idan an yi ɗafa-ƙeya?
Amsa: - Jibson

**Auna fahimta ta biyu (2)**

1- Me ake nufi da Ɗafa-ƙeya?

Amsa: - ɗafa-ƙeya ɗafi ne wadda ake liƙawa a ƙarshen kalma

2- Kawo sunayen Hausawa uku da ake yi masu ƙirar Ɗafa-ƙeya.
Amsa: -
i- Umma
ii- Amina
iii- Jamila
iv- Salma da sauransu

3- Kawo cikakken sunayen Hausawa.

i- Ummancy
ii- Aminancy
iii- Nafisancy
iv- Salmancy

Amsa: -

i- Umma
ii- Amina
iii- Nafisa
iv- Salma

4- Ya ya sunan Rabiya zai kasance idan an yi ɗafa-ƙeya?
Amsa: - Rabiyancy

## Kashi na uku (3) Sunayen Hausawa na Dangantaka

**Abubuwan da Suke Ciki**

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufar Darasi
3.3 Dangantaka
 3.3.1 Sunayen Dangantaka na Hausawa Maza
 3.3.2 Sunayen Dangantaka na Hausawa Mata
3.4 Taƙaitawa
3.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
3.6 Manazarta
3.7 Amsoshin Auna Fahimta

## 3.1 Gabatarwa

A cikin kashin da ya gabata, mun gabatar da bayanai kan sunayen da Hausawa suke sanyawa 'ya'yansu, waɗanda sun samu ne a sanadiyyar wayewa da ilimin boko. Matasa (maza da mata) su ne suke ƙirƙirar sunayen ta hanyar yin wata 'yar kwaskwarima sannan, su yi amfani da su a matsayin sunayen Hausawa a harshen Hausa. Amma a wannan darasin za mu yi bayani ne kan yadda ake samar da sunayen Hausawa na dangantaka.

## 3.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan rukuni ɗalibai za su iya:

- Bayani kan Ma'anar Dangantaka.
- Zayyana Ire-Iren Dangantaka.
- Zayyana sunayen Hausawa ta hanyar Dangantaka.
- Bambace sunayen maza da na mata ta fuskar Dangantaka.

## 3.3 Dangantaka (relationship)

Kalma ce da take nuna kusanci ko 'yan'uwantaka da take tsakanin wani da wani ko wata da wata ko kuma wasu da waɗansu. Akwai danganta iri-iri kamar dangantaka ta jini da ta aure da kuma makwabtaka.

### 3.3.1 Sunayen Dangantaka na Hausawa Maza

Akwai sunayen Hausawa maza na dangantaka wadda ta shafi jini. Irin wannan tsarin suna yana farawa daga tushe ko asalin zuwa inda aka tsaya ma'ana, tun daga kaka har zuwa jika ko jikoki ko tattaɓa kunne da sauransu. Ana yin amfani da irin waɗannan sunayen Hausawa ga mutanen da suke dangantaka ta jini. Ga su kamar haka:

| Suna | Ma’ana |
|---|---|
| Kaka | Mahaifin uwa ko uban mutum |
| Uba | Mahaifin mutum |
| Kawu | Ƙanin mahaifi ko mahaifiya |
| Wa ‘yaya’ | Wanda aka riga haifa kafin wani ko wata ko wasu ‘yan ɗaki ɗaya ko ‘yan uba |
| Ƙani | Wanda sai da aka haifi wani ko wata sannan aka haife shi |
| ɗa | Yaron da mutum ya haifa |
| Jika | ’Yan da wani ko wata ya/ta haifa sannan shi ma ko ita ma ya/ta haifi ɗa |
| Auta | Ɗan da aka haifa a ƙarshen |

**Auna fahimta ta farko (1)**

1- Me ake nufi da ƙira Dangantaka?
2- Kawo sunayen Hausawa na dangantaka guda uku.
3- Kawo ma’anar waɗannan sunayen.
i- Kaka
ii- Uba
iii- ɗa
iv- jika
4- Wacce dangantaka ce tsakanin kaka da jika?

## 3.3.2 Sunayen Dangantaka na Hausawa Mata

Akwai sunayen Hausawa maza na dangantaka wadda ta shafi jini. Irin wannan tsarin suna yana farawa daga tushe ko asalin zuwa inda aka tsaya ma’ana, tun daga kaka har zuwa jika ko jikoki ko tattaɓa kunne da sauransu. Ana yin amfani da irin waɗannan sunayen Hausawa ga mutanen da suke dangantaka ta jini. Ga su kamar haka:

| Suna | Ma’ana |
|---|---|
| Kaka | Mahaifin uwa ko uba |
| Uwa | Mahaifiyar mutum |
| Gwaggo | Ƙanin mahaifi ko mahaifiya |
| Ya/yaya | Wadda aka riga haifa kafin wani ko wata ko wasu ‘yan ɗaki ɗaya ko ‘yan uba |
| Ƙanwa | Wadda sai da aka haifi wani ko wata sannan aka haife ta |
| ’Ya | Yarinyar da mutum ya haifa |
| Jika | ’Yan da wani ko wata ya/ta haifa sannan shi ko ita ma ya/ta haifi ɗa |
| Auta | ’Yan da aka haifa a ƙarshen |

Daga cikin sunayen da aka kawo a sama, akwai wasu sunaye waɗanda za a ga cewa a kowanne ɓangare( maza da mata) duk iri ɗaya ne sai dai sun bambanta ta waje amfani da su, misali:

i- Kaka – mace ko namiji
ii- Jika - mace ko namiji
iii- Auta – mace ko namiji

**Auna fahimta ta biyu (2)**

1- Kawo sunaye uku waɗanda maza da mata suke amfani da su.
2- Kawo sunayen Hausawa na dangantaka na mata guda uku.
3- Yi bayanin ma'anar waɗannan sunaye.
i- Kaka
ii- Uwa
iii- 'Ya
iv- Ƙanwa
1- Wacce dangantaka ce tsakanin Uwa da Auta?

## 3.4 Taƙaitawa

A wannan kashin, mun kawo bayani kan sunayen Hausawa waɗanda ake samarwa ta hanyar amfani da dangantakar da take tsakanin mutanen. Irin waɗannan sunayen ana amfani da su a tsakanin al'ummar Hausawa. Sannan mun kawo misalai na sunayen Hausawa na dangantaka na maza da kuma na mata. A ƙarshe, mun kawo tambayoyin da za a amsa.

## 3.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi

Dangantaka – Kalma ce da take nuna kusanci ko 'yan'uwantaka da take tsakanin wani da wani ko wata da wata ko kuma wasu da waɗansu
Jika–'Ya/ɗan da wani ko wata ya/ta haifa sannan shi ma ko ita ma ya/ta haifi ɗa

Auta - 'Ya/Ɗan da aka haifa a ƙarshen

## 3.6 Manazarta

Abdullahi I.S.S (2008). "Jiya ba Yau Ba: Waiwaye a Kan Al'adun Matakan Rayuwar

Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa." Kundin digiri na uku: Jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto.

Adamu, M. T. (2015). Tasirin Musulunci Kan Sunayen Hausawa. A Cikin *Harsunan Nijeriya*, Vol. XXV: 163-186.

Alhassan da Wasu (1987) *Zaman Hausawa*. Zaria: ABU Press.

Amfani, A.H. (2007). Hausa Morphology. In *Basic Linguistics for Nigerian Languages Teachers.* (ed) Ore Yusuf. Port Harcourt: M&J Grand Orbit Communication Ltd.

Bichi A.Y (2013). *Tsokaci a Kan Bukukuwan Hausawa na Gargajiya wajen cigaban*

*Al'umma*. Zaria: Ahmadu Bello University, Press.

CNHN (1981). *Rayuwar Hausawa*. Lagos: Thomos Nilson Nigeria Limited.

Gwammaja, I. G. (nd). Tsokaci Kan Tasarifi a Cikin Waƙoƙin Dakta Mamman Shata.

Gusau, G.U (2012). *Bukukuwan Hausawa*. Gusau: Ol-Faith Prints.

Plag, I. (2002). *Word-Formation in English*. Siegea: Cambridge University Press.

Sani, Ɗ. (2002) Word- Formation in Hausa (A case study of derivation Functional shift and clipping) Ph. D dissertation. Bayero University, Kano.

## 3.7 Amsoshin Tambayoyin

Auna fahimta ta farko (1)

1- Me ake nufi da ƙira Dangantaka?

Amsa: -
Kalma ce da take nuna kusanci ko 'yan'uwantaka da take tsakanin wani da wani ko wata da wata ko kuma wasu da waɗansu. Akwai danganta iri-iri kamar dangantaka ta jini da ta aure da kuma makwabtaka.

2- Kawo sunayen Hausawa na dangantaka guda uku.
- i- Kaka
- ii- Uwa
- iii- Uba
- iv- Ƙanwa
- v- Auta da sauransu

3- Kawo ma'anar waɗannan sunayen.
- i- Kaka
- ii- Uba
- iii- Ɗa
- iv- Jika

Amsa: -
- i- Mahaifin uwa ko uba
- ii- Mahaifi
- iii- Ɗan da aka haifa bayan an yi aure
- iv- 'Yan da wani ko wata ya/ta haifa sannan shi ko ita ma ya/ta haifi ɗa

Wacce dangantaka ce tsakanin kaka da jika?

Amsa: ta jini

**Auna fahimta ta biyu (2)**

1- Kawo sunaye uku waɗanda maza da mata suke amfani da su.

Amsa: -

- i- Kaka
- ii- Auta
- iii- Jika

2- Kawo sunayen Hausawa na dangantaka na mata guda uku.
Amsa:

i- Uwa
ii- Uba
iii- Ɗa
iv- ’Ya da sauransu.

3- Yi bayanin ma’anar waɗannan sunaye.

i- Kaka – mahaifin uban mutum
ii- Uwa – mahaifiyar mutum
iii- ’Ya – yarinyar da mutum ya haifa
iv- Ƙanwa – yarinyar da aka haifa bayan an haifi wani ko wata.

Wacce dangantaka ce tsakanin Uwa da Auta?
Amsa: - jini